# Bayanan Wayewa

# Musulunci a Sauk'ak'e

# Na biyu

# Tsararrun Darussa Cikin Fik'ihun Musulunci

Wallafar:

Sayyid Riyad Al-Hakeem

Darul – Hilal

Offishin Mai Girma Babban Marja'i

SAYYADI ALHAKEEM

*Hak'k'in Bugawa Na Mai Mallaka Ne*

*Bugu Na Farko*

*1433 H – 2012 M*

*Cibiyar Al'adun Musulunci Take Yad'awa*


*Ofishin Mai Girma Marja'in Addini Mai*

*Girma Sayyid Hakim (d)*

- **IRAQ** - **Alnajaf alashraf**
  Tel.333180 - 370046 (33 964+) :.
- **IRAN** - **Qum** - P.O.Box 486/37185 :
  Tel - 7740230 (251 98+) :Fax.7742146 (251 98+) :
- **Syria** - **Damascus** - **Sayeda Zaynab) a.s(**
  Tel - 6470752 (11 963+):.Fax.6472058 :
- **Lebanon** - **Beirut**
  Tel - 451634 (1 961+):.Fax.451635 (1 961+) :

Website :http//:www.alhakeem.org
com.alhakeem@info :mail.E

Hakim, Riyad, 1958
Tsararrun Darussa Cikin Fik'ihun Musulunci /
Mawallafi Sayyid Riyad Hakim; kula de tarjama Munir Muhammad Sa'id -Qum: Dar al Helal,2010-1431H
P:166

ISBN: 978 – 964 – 8276 – 91 – 6 10000 Rials

الفهرسة طبق نظام فيپا. المصادر بالهامش.

العنوان الأصلي: دروس منهجية في الفقه الإسلامي

1. Islamic law jafari-20th century. I. Said Munir Muhammad. II. Title
297.342 BP 183.5 . H2t504952

رقم المكتبة الوطنية: 2973426

*Sunan Littafi:* *Tsararrun Darussa Cikin Fik'ihun Musulunci*

*Mawallafi:* *Sayyid Riyad Hakim*

*Kula Da Tarjama:* *Munir Muhammad Sa'id*

*Sake Dubawa:* *Hafiz Muhammad Sa'id*

*Bugu* *Na farko*

*Mabuga:* *Fadhil*

*Adadi Kwafi:* *1000*

*Tarihin Bugu:* *1433 H. 2012 M, 1391 H.Sh*

*Mai Yad'awa:* *Darul Hilal*

*ISBN: Lambar Wallafa: 978 – 964 – 8276 – 91 – 6*

بسمه تعالى

*Godiya ta tabbata ga Allah (s.w.t) Kuma Aminci ya k'ara tabbata ga bayinsa wad'anda ya zaba*

# *Da sunan Allah Mad'aukaki*

## *An tabbatar da duba wannan littafin da kuma aiwatar da shi ne bisa dacewar fatawoyin mai girma babban Marja'i Makomar addini Sayyid Al-hakeem (Allah ya tsawaita rayuwarsa)*

*Kwamitin Fatawa Na Ofishin Mai Girma Babban Marja'in Makomar Addini Sayyid Muhammad Tabataba'i Al-Hakeem*

**23 Jimada Auwal 1415**

**Sadaukarwa**

Zuwa miliyoyin mabiya ‘ya’yan gidan Annabin Allah Muhammad (Amincin Allah ya tabbata gare su) da Malamai masu tsoron Allah waxanda suka ba da gudummawa wajen fuskantar da al’umma da kare ta daga zamewa da kaucewa hanya, suna masu qalubalantar dukkanin wasu nau’o’in fitintunu da qeqashewar zuciyar masu karkatarwa, da ‘yan ta’adda.

Da Shahidai waxanda xagutan zamani suka cika maqabartun mutane na sarari da kwazazzaban **"Iraqi"** da su, da kuma waxanda jikkunansu masu tsarki suka zagwanye a cikin daro-daro da durarrukan narkar da naman xan Adam, haka ma waxanda gavovinsu suka yi xai-xai ta hanyar datsewa da dai sauran kayayyakin azabtarwa na zamani.

Da kuma sauran waxanda suke tsare wanxannan da suka fuskanci hukumar "Sadam Husain" da zabaniyawanta marasa imani da tausayi a cikin kurkukun qarqashin qasa mai ban tsoro, amma ba su taxa canzawa ba.

## Gabatarwa

Fiqihun Musulunci yana taka babbar rawa a fagen wayerwa a Musulunci wanda yake qunshe da kaso mai yawa na ayoyin Kur'ani mai girma da kuma wani adadi babba na Sunnar Annabi mai girma da suke xauke da bayanin hukuce-hukuncen Fiqihu, kuma musulmi sun himmatu da wallafe-wallafe masu yawa da qima na Fiqihu, a fagen kafa dalilai ne ko kuma na fatawa.

Duk da cewa wannan littafin namu bai isa ga waxannan martabobin da aka ambata ba bisa lura da cewa littafin ne na Fiqihu mai sauqi, domin tattaro bayanin fiqihun Musulunci, daidai da mahazabar nan ta 'ya'yan gidan Annabi Aminicin Allah ya tabbata a gare su, saboda Samari da matasa, sai dai (wannan littafin) yana da wata qebantuwa ta musamman wacce yana da wahalar gaske ka same ta a waninsa, bisa la'akari da cewa shi littafin an wallafa shi ne a cikin wani yanayi mai wahala na musamman, wato lakacin da muka shafe a tsare a cikin kurkuku, da sauran iyalanmu, daga cikin su akwai waxanda suka yi shahada a wancan lokacin, a gefe guda kuma akwai dubban matasa muminai waxanda suke cikin qishirwar su

sami wayewa a kan hukuncin shari'a na Fiqihu.

Duk da qeqashewar zuciyar xagutan, da tsananin sa idon su, da kuma haxarin nan mai muni da yake kewaye da mu domin kuwa dukkanin wani qoqari da mutum zai yi na wayar da mutane game da addini, to yin hakan na jawo masa hukuncin kisa a qarqashin tsarin Saddam, sai dai tare da haka a sakamakon jin sauke nauyin addini da kuma buqatuwa mai tsanani da ake da ita a wannan guri, shi ya sa na wallafa littattafai guda biyu tare da buga su, da kuma yaxa su tare da karantar da su a voye cikin xakunan da suke kukkule da muka sami kawukanmu a ciki waxanda suke a qarqashin vangaren doka ta musamman na kurkukun "Abu Guraib" da ke yammacin "Bagdad", Amma da yake littafin farko ya kasance ya vace sakamako binkice mai tsanani na ba zata da azzalumai masu sa ido na jami'an tsaro suka gudanar, a yayin da Allah ya qaddara wa littafin na biyu wanzuwa, wanda shi ne wannan littafin wanda na rubuta shi da yare mai sauqi, domin waxanda ake magana da su a cikin littafin su ne matasa waxanda suke farkon shekarun samartakarsu, duk da cewa fa qeqasasshen yanayin tsaron wannan lokaci ya kasance yana hana muminan Iraqi kai kawo wajen

waxanda suka yi saura na daga Malamai da xaliban zauran karatun ilimin addini da kuma amfanuwa da su, sai na xau mataki na gaba wato: wallafar wannan littafin tare da kwafarsa da tseratar da shi daga cikin kurkukun zuwa waje, -saboda ya toshe waccan damar, saboda haka mai karatu zai ga an taqaita shi ne a kan babobin fiqihun da suka shafi jama'rar matasa, -a yayin nan ne wasu daga cikin mumunai suka karve shi, suka kuma yaxa kwafofin sa masu yawa ga sauran nahiyoyin Iraqi.

Bayan faxuwar tsarin xagutu da samun damar cike buqatar 'ya'yan mu maza da mata game da sanin hukunce-hukuncen addini, sai na ga na sake bibiyar littafin domin buga shi, saboda sake tunatar da matasanmu maza da mata game da wahalhalun da 'yan mazan jiya da suka gabata suka fuskanta, da kuma dagewarsu a kan sanin hukunce-hukuncen fiqihu, duk da qeqasar yanayoyin da suka shuxe da su, da kuma haxarorin da ke kewaye da su, ta yiwu wannan ya taimaka wajen qarfafar su a wajen jin sauke nauyin da yake kan 'yan mazan yau da kuma gode wa ni'imar Allah da ya yi musu na kuvuta daga xagutu da tsarinsa, ina mai roqon Allah

maxaukaki da ya cika ni'imarsa ga Iraqi da Iraqawa na kuvuta daga wutar mamayar 'yan mamaya, ya kuma datar da su wajen gina garuruwansu masu maxaukaka kuma ya qara danqon alaqarsu a qarqashin inuwar addininsu mai tushe.

Haqiqa an xora wannan littafin a bisa doran fatawowin mai girma Sayyid mahaifina (a.y.z), tare da wasu qare-qare masu sauqi, kuma na kira shi da sunan koyarwar Fiqihun Musulunci a cikin tsari domin ya xauki matsayi na biyu na jerin salsalar littattafan wayer da kai a bisa, Musulunci a sauqaqe, don ya zama littafi na biyu a bayan na xaya-Kan Aqida-domin su zama jerin salsalar sauqaqqun qananan littatafan wayar da kan musulmai, ina mai roqon Maxaukaki (s.w.t) da ya sanya shi an yi ne don zatinsa mai girma, ya kuma amfanar da matasa da shi, domin shi maxaukaki ne mai ji kuma mai amsawa.

Hujjatul Islam Sayyid **Riyad Al-Hakeem**

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin Qai

Akwai wasu al'amura da suka wajaba a kan Musulmi ya yi imani da su, kuma ana kiran su da tushen addini.

## Tushen Addini

Tushen addini gusa biyar ne:-

1- Kaxaituwar Ubangiji

2- Adalcin Allah

3- Annabtar Annabi

4- Shugabancin Imami

5- Makoma "Lahira"

a) Kaxaitar Ubangiji Ma'anarsa shi ne cewa Allah shi kaxai ne, shi ne wanda ya halicci duniya da duk abin da yake cikinta na doran qasa da sararin samaniya da rana da wata da mutum da kuma dabbobi d.s.s.

b) Adalcin Allah Ma'anarsa shi ne cewa Allah adali ne ba ya zaluntar kowa, ya kuma sanya ladansa ga waxanda suka yi aiki na gari, azabarsa kuma ga waxanda suka sava masa.

c) Annabtar Annabi ma'anarta ita ce Allah maxaukaki domin ya shiryar da mutane zuwa ga alheri ya nisanta su tare da hana su yin sharri da munanan ayyuka, ya umarci sashen wasu mutane na gari ya xora musu sadar da saqonsa zuwa ga xan Adam, ana kiran wannan mutumin da Annabi ana kuma ambatonsa da manzo. Annabawa suna da yawa, na farkonsu shi ne; Adam (a.s), sai Nuhu (a.s) da Ibrahim (a.s), da Musa (a.s), da kuma Isa (a.s), sai kuma na qarshensu Annabinmu Muhammad xan Abdullahi (s.a.w), Allah ya aiko shi da Addinin Musulunci, duk wanda ya yi imani da shi, ya kuma yi imani da saqonsa ana kiransa Musulmi, mu musulmai ne saboda mun yi imani da Annabi Muhammad (s.a.w) da abin da ya zo dashi, addinin Musulunci.

d) Shugabancin Imamai yana da ma'anr cewa Annabi Muhammad Amincn Allah ya qara tabbata a gareshi da 'ya 'yan gidansa, tabbas ya kafa Na'ibi wanda zai wakilce shi a wajen shiryar da mutane a al'amuransu wanda ake kiransa da

(IMAMI)

shugabannin da aka kafa su goma sha biyu ne bisa jerin nan mai zuwa:

Imam Aliyu Ibn Abi Xalibi Amincin Allah ya tabbata a gareshi wanda aka binne a Najaful Asharaf "**Iraqi**".

Imam Hassan Dan Ali tsarkakakke, Amincin Allah ya tabbata a gareshi wanda aka binne a Madina mai haske.

Imam Hussaini Shahidi, wanda aka binne shi a Karbala mai tsarki "**Iraqi**".

Imam Muhammadul Baqir amincin Allah ya tabbata a gareshi wanda aka binne shi a garin Madina mai haske.

Imam Ja'afar Sadiq, amincin Allah ya tabbata a gareshi wanda aka binne a Madina.

Imam Musa Al-Kazim, Amincin Allah ya tabbata a gareshi, wanda aka binne a Bagdad Birnin Kazimiyya.

Imam Aliyu Arridha wanda aka binne a Kurasan Mash'had (Iran)

Imam Muhammad Al-jawad, amincin Allah ya tabbata a gareshi, wanda shi ma aka binne shi a Bagdad (Kazimiyya).

Imam Aliyu Al-Hadi, amincin Allah ya tabbata a gareshi an binne a garin Samra' " a **Iraqi**.

Imam Hassan Al Askari, Amincin Allah ya tabbata a gareshi shi ma an binne shi a Samra'.

Imam Muhammad Al-Mahdi, amincin Allah ya tabbata a gareshi ya kuma gaggauta bayyanarsa, shi ne Imamun mu na yanzu a wannan zamani, ana kiransa da imamin Zamani, hujjar Allah akan mu, yana a halin vuya, zai bayyana da iznin Allah, domin ya yaxa adalci a bayan qasa.

Duk wanda ya yi Imani da shugabancin waxannan Imamai to shi shi'a ne xan Imamiyya goma sha biyu, mu shi'ar Ahlul Baiti saboda, mun yi Imani da shugabancin su kuma mun yi Imani da su.

e) Makoma (Lahira) ita kuma ma'anar ta, ita ce cewa, tabbas Allah zai raya mutane bayan sun mutu ya yi musu hisabi a ranar Al-qiyama ya shigar da waxanda suka bi suka yi aiki na gari Aljannar da a cikinsu akwai dukkanin abin da

mutum yake sha’awa yake so, ya kuma shigar da mutanen banza waxanda suka yi savo a cikin wuta su azabtu a cikinta.

Abin da aka wajabta shi ne, lalle mu riqa yiwa Allah biyayya da xa'i tare da riqo da hukunce-hukuncen addini, kamar Sallah, Azumi da Makamantansu, kamar yadda da sannu za mu bayyanasu, mu kuma siffanta da siffofi ababen yabo, irin su gaskiya, riqon amana, da kuma adalci, har sai Allah ya yarda da mu, ya kuma shigar da mu Aljanna tare da Annabawa da Imamai da Sahhidai da dukkanin mutanen na gari (salihai).

**Rassan Addini**

Su ne hukunce-hukuncen addinin Musulunci wanda aka wajabta a kan dukkanin musulmi da ya yi riqo da su mahimmai daga ciki su ne:

1 Sallah 2 Azumi 3. Hajji 4. Kumusi 5. Zakka 6. Jihadi 7. Umarni da kyakkyawa 8. Hani da abin qi 9. Jivanta: wato jivantar Manzo, amincin Allah ya tabbata a gareshi da kuma jivintar Imamai, amincin Allah ya tabbata a garesu a bayan sa, haka nan da jivintar lamarin muminai bisa lura da Imaninsu. 10. Yin Bara'a: shi ne mutum ya qi Maqiya Allah na daga Kafirai da Azzalumai waxanda suka kaucewa gaskiya.

TAMBAYOYI

1- Mene ne ma'nar Tauhid?

2- Mene ne ma'anr Adalci?

3- Wane ne Manzo?

4- Kawo adadin sunayen Annabawa goma?

5- Waye farkon Annabawa da kuma na qarshe?

6- Wane ne ya kafa Imam Ali, Amincin Allah ya tabbata a gareshi?

7- qirgo sunayen Imamai, Amincin Allah ya tabbata garesu?

8- Mene ne ma'anar Makoma?

9- Mene ne tushen addini, saboda me ake kiran su da tushen addini?

10- Qirgo mihimmai daga cikin rassan addini guda goma?

11- Ka faxi wani lokaci wanda wanda a cikinsa ka yi hani da abin qi?

12- Shin kana riqo da yin umarni da kakkyawa? Ka faxi wani lokaci da a cikinsa ka yi umarni da abu mai kyau?

13- Ahmad yaro ne mai ladabi kuma abin so, saboda yana riqo da Sallarsa yana riqo da nasihun iyayensa, abin lura shi ne Abokinsa yakan yi qarya ga Mahaifiyarsa, sai Ahmad ya hana shi ya kuma yi masa gargaxi da cewa idan ya qara qarya nan gaba to zai rabu da shi ba kuma zai qara yarda

da abokantakarsa ba, shin wannan umarni ne da kyakkyawa ko kuma hani da abin qi?

14- Mene ne ma'nar Jivanci da bara'a?

15- Mu muna son Hussaini, Amincin Allah qara tabbata a gareshi, sannan muna qin Yazidu xan Mu'awiya wanne ne a cikinsu Jivinta wanne ne kuma Bara'a?

**Alamomin Balaga Na Shari'a**

Balagar yaro tana da alamomi guda uku, su ne:

1- Ya cika shekara goma sha biyar (15) bisa tarihin hijirah wanda shi ne ya yi daidai da shekara goma sha huxu (14) da wata shida da rabi lissafi mafi kusa na tarihin wata.

2- Yin mafarki yayin da yake bacci ta yadda nau'in nan na Maniyyi yakan fita a sakamakon yin mafarkin da ya yi a lokacin da yake baccin ko kuma wani dalilin na daban.

3- Bayyanar gashi mai kauri a fuska ko kuma a kan makafarsa, (gefen al'aura daga sama).

Ana iya isuwa don tabbatar da balagar yaro ta hanya xaya daga cikin alamomin nan guda uku, ko da kuwa sauran alamomin guda biyu basu tabbata ba.

Idan yaro bai gane cewa ya balaga ba, to a bajiro da maganar ga xaya cikin Magabatansa daga a halinsa kamar babbansa ko yayansa, sai ya yi masa bayani.

Alamar balagar 'ya mace kuwa xaya ce: ita ce cikar ta shekara tara (9) a bisa tarihin hijira wanda shi ne ya yi daidai da shekara takwas (8) da wata takwas (8) da kuma kwana ishirin (20) a lissafi mafi kusa.

Mas'ala ta Daya (1): idan yaro ko yarinya ta balaga a Shari'a to daga nan matakin quruciya ya kare, ya zama wajibi su lazimci hukunce-hukuncen Shari'a daga nan sai su riqa sauke wajibobi su kuma riqa hanuwa daga abubuwan da suka haramta, hukuncinsu kamar na manya ne, Allah zai riqa yi musu Hisabi a kan ayyukansu, zai kuma riqa gode musu a kan biyayyar da suke masa, kuma za a riqa rubuta musu ladan mai yawa ranar alqiyama. Abin da ya kamata shi ne, su riqa aikata sashen wasu Mustahabbai domin ladansu ya qaru, kamar taimakon talaka da ziyartar Masallatai da Makwancin Annabi Amincin Allah ya tabbata a gare shi, da yin Addu'a da yin karatun Kur'ani da aiwatar da sashen wasu nafilfili, idan yaro ko yarinya ba su san haka ba, su tambayi wasu domin kada ladan waxannan ayyuka su kuvuce musu, a qarshe kafin hakan su riqa dogara ga Allah Maxaukaki tare da neman taimakonsa, a kan dukkannin lamurransu. domin

shi Allah maxaukaki, abin Madalla ne da kasancewarsa majivinci, kuma madalla da shi mai taimako.

**Ijtihadi (Qoqari) Da Taqalidi (Bibiyar Fatawa)**

A baya mun ce dole ne a kan Musulmi ya yi riqo da rassan addini da kuma sauran dukkanin hukunce-hukuncen addinin Musulunci waxanda Allah ya yi umarni da su domin Allah ya yarda da shi, ya kuma shigar da shi Aljanna bayan ya mutu, sai dai akwai wata matsala da suke fuskantar mu kamar haka:

Lallai Annabi, Amincin Allah ya tabbata gareshi wanda shi ne wanda Allah ya isar masa da addinin Musulunci, haqiqa ya yi wafati tun kafin shekara ta dubu xaya da xari huxu (1400) to ta yaya zamu san hukunce-hukuncen Addinin, idan har ya zamo Manzo amincin Allah ya tabbata a gareshi da Imamai amincin Allah ya tabbata a gare su, ba sa tare da mu.

A saboda mu warware wannan matsalar za mu iya cewa: A tsawon shekaru da suka gabata akwai malaman da suka yi ilmin addini suka kevanta da shi ta yadda suka samu damar sanin hukunce-hukuncen Shari'a, waxannan malaman ana kiran su Mujtahidai.

Mujtahidi shi ne wanda ya san hukunce-hukuncen addinin, wanda wajibi ne mu riqa tambayarsa mu riqa tuntuvar fatawoyinsa tare da riqo da su, wannan shi ne ma'anar Taqlidi, kenan; taqlidi shi ne yin aiki na ibada da na mu'amala dai dai ra'ayin Mujtahidi.

Ta yiwu wani ya tambayi cewa; saboda me ba za mu bi wanda ba Mujtahidi ba a cikin sanin hukunce-hukuncen addini?

Amsa ita ce: Babu wanda ya san hukunce-hukuncen addini sai Mujtahidi saboda haka ba za mu bi waninsa ba, ba zamu bi wani xan Kasuwa ko Likita ko Magini da harkar wutar lantarki ko waninsu ba.

Misali, Likita ya karanci ilimin Likitanci ya kuma kevanta da shi, wannan ya sa muke komawa gareshi yayin rashin lafiya, muke riqo da abin da ya nuna ba za mu tava bin umarnin waninsu a wajen magance rashin lafiya ba. Magini ya karanci ilimin gine gine ya kuma ya kevanta da shi, shi ne yake kulawa da gina manya manyan gine-gine da gadoji. Kenan a kowane fage muna komawa zuwa ga Malamin da ya kevanta da ilimin wannan fage, saboda haka ya kamata mu

riqa komawa zuwa ga Mujtahidi a cikin sanin hukunce-hukuncen addini.

Mas'ala ta 2: Ya wajaba mujtahidin da mutum zai yi taqlidi da shi ya cika sharaxai muhimmai guda biyu.

1- Ya kasance a qarashen martaba ta adalci wato ya zama mai bin Allah, sau da qafa, kuma mai yin riqo da hukunce-hukuncen addini.

2- Ya kasance mafi ilimin zamaninsa, kamar yadda maras lafiya yake zavar likitan da yafi kowanne, haka nan ya wajaba ga Mutum ya zavi wanda yafi sauran Mujtahidai Ilimi, domin ya riqa taqlidi da shi a cikin ayyukansa.

Mafi ilimi shi ne wanda yafi waninsu sanayya game da hukunce-hukuncen addini wanda aka kira da hukunce-hukuncen Sahri'a.

Mas'ala ta uku (3) ya mai girma ka iya tambaya cewa: Ta yaya zan san cewa Mujtahidi wane shi ne ya fi ilimi?

Amsar ita ce: Akwai Malaman da suke sun kevanta da sanin ilimomin addini, sai ka tambayi xaya daga cikin managartan Malaman ya ba ka

amsa da cewa Mujtahidi wane ne, kuma shi ne wanda ya fi kowa ilimi a kan sauran sai ka yi taqalidi da shi.

Idan kuwa wasu daga cikin danginka ko kuma abokanka sun xauke maka nauyin tambayar Malaman dangane da cewa wane ne Mujtahidin da ya fi kowa ilimi, zai yiwu ka dogara da shi, sai dai ya wajaba a gareka ka tabbatar da cewa abokin naka tabbas a wannan lokacin ya tambayi xaya daga cikin Malaman da suke masana kuma amintattu a kan hakan, idan ko bai tambayi Malamin da ya cancanta da hakan ba! To kada ka dogara da gamsuwarsa ta qashin kansa, saboda bai san waye mafi ilimi ba saboda rashin kebantuwarsa da ilimin addini.

TAMBAYOYI

1- Wane ne Mujtahidi?

2- Saboda me muke riqo da Mujtahidi a hukunce-hukuncen addini?

3- Ka faxi sharaxin nan biyu manya game da Mujtahidi tare da sharhinsu?

4- Ta yaya zamu san Mujtahidi wane shi ne ya fi kowa ilimi?

5- Idan abokinka ya ce Mujtahidi wane shi ne ya fi kowa ilimi, ba tare da cewa shi abokin naka a haqiqa ya tambayi Malamai ba, shin zaka dogara da zancensa ko kuma zaka tambayi waninsu?

**Najasosi**

Aqwai wasu abubuwa na qazanta da bai halatta ga musulmi ya riqa ci ko shan xaya daga su ba, kamar yadda yake wajibi a kansa ya gusar da su kuma ya tsaftace (tsarkake) Jikinsa da tufafinsa daga gare su a yayin da zai yi salla. Ana kiran su da najasosi. Adadinsu guda goma ne kamar haka:-

Na xaya da na biyu:- Fitsari da gayaxi (abin da ya fita daga mutum) dukkaninsu najasa ne, haka ma bawali da bahayan dabbobi idan sharaxai uku saka tabbata a kan su:

1- Jininsa ya riqa ingizowa-wajen fita-yayin da aka yanka shi, ya zama ba ya fita a hankali, kuma ya zama yana tsartuwa wato yana da jijiyoyin da jini yake kwarara lokacin da aka yanka shi.

2- Ya zama haram ne cin namansa.

3- Kada ya zama wanda yake tashi sama (sararin samaniya).

Misalin kerkeci, dukkanin waxannan sharaxan uku sun cika a kansa, domin jini yana fita da ingizar yayin da aka yanka ta, kuma haramun ne

cin namansa a Musulunci, kuma ba ya daga cikin wanda suke tashi sama. Don haka bawalinsa da burotsonsa najasa ne.

Amma idan ya zama xaya daga cikin waxannan sharaxan bai cika ga dabba ba, fitonta (bawalinta da gayaxin ta) ba su zama najasa ba, misali Kifi jininsa yana naso ko kwarara (wato fita a hankali) amma ba ya ingizowa da qarfi yayin fita, rago kuwa ya halatta a ci naman sa. Jemage da shirwa ko shaho su kuma suna tashi sama.

Saboda haka waxannan kalolin dabbobi guda uku da muka ambata da makamancinsu, tun da sharaxan nan gudu uku ba su cika a kan su ba, to bawalinsu da gayaxinsu tsarkakku ne.

Mas'ala ta huxu (4): Idan ya zama akwai wata dabba da ba a sami ikon sanin cewa sharaxan nan guda uku (3) sun tabbata a kanta ko ba su tabbata ba, za a yi hukunci tsarkin bawalinta da kashin ta.

Na Uku (3): Maniyin Mutum, haka nan da maniyin dabba da sharaxin jininta ya riqa ingizar juna da qarfi yayin da aka yanka ta, amma ba ya naso,-fita a hankali-, kuma kada ya zama wanda ake cin namansa, don haka maniyyin wannan dabbar najasa ne.

Na huxu: Mataccen mutum, haka ma matacciyar dabba, da sharaxi guda xaya: shi ne jinin ta ya riga ingizar juna da qarfi yayin da aka yanka ta, amma ba ya naso, (fita a hankali), da za mu sami dabba matacciya kamar rago to wannan najasa ne, haka nan da za a yanka dabba ba ta hanyar da Musulunci ya ce ba, misali; dabbar da kafiri ya yanka, najasa ce.

Amman mushen kifi tsarkakke ne saboda jininsa a hankali yake fiya, kuma ba shi da jijiyoyin da jini yake tsartuwa daga gareshi.

Mas'ala ta Biyar (5): Duk dabbar da jinin ta ba ya kwarara yayin da aka yanka ta mushenta tsarkakke ne kamar dangogin fari da kifi da qwaxi, haka nan dabbar da ba masaniyar cewar jininta yana kwarara ne ko naso yake yi a yayin da aka yanka ta, to za a yi musu hukunci da tsarkin mushensu.

Mas'ala ta Shida (6): Namomi da Fatocin da ake samu a garuruwan Musulunci ya halatta a yi amfani da su wajen ci da sanyawa saboda salla. Idan babu masaniyar cewa kafiri ne ya yanka dabbar, haka nan da ace an zo da su daga garuruwan kafirai ne amma Musulmi, mumini ne

yake sayar da su, wanda yake mai riqo da hukunce-hukuncen addini, don haka la'akari da kulawarsa da himmatuwarsa wajen tabbatar da tsarkakuwarsu ya isar wajen yin hukunci da tsarkinta, a shari'ance.

Mas'ala Bakwai (7) Namomi da Fatoci da aka saba da su, da ake samu a garuruwan Musulunci idan babu masaniyar cewa na gida ne ko kuma an zo da su daga waje ne to su ma tsarkakakku ne ya halasta cin su da sanya su domin salla, haka nan Fatocin da ake qirqira da aka yi su a qasashen kafirai su ma tsarkakakku ne.

Na Biyar (5): Jinin Mutum haka nan na dabbar da in an yanka ta yake kwarara ba mai naso ba, kamar jinin rago da na tsuntsaye, amma idan ya zama jinin dabbar yana xixxiga yayin da aka yanka amma ba ya kwarara, kamar jinin kifi da na kwaxo da kuma na qwari kamar na kaska da na quda to tsarkaka ne.

Mas'ala ta Takwas (8): Idan ka ga jini a jikin tufarka amma ba ka da masaniya cewa jikinka ne ko kuma na wasu qwari ne, to mai tsarki ne.

Mas'ala ta Tara (9): Jinin da ya kan kasance a cikin qwai a cikin wani siririn marufin nan mai

tsarki ne, sai dai a bisa Ihtiyaxi na wajibi haramun ne cin sa.

Mas'ala ta Goma (10): Jinin da yake gudana daga dabba yayin da ake yanka ta najasa ne, amma wanda ya saura a jikin abin yankan bayan an yanka, mai tsarki ne, don haka zai iya yiwa a tsarkake wuyan abin yanka bayan yankan, haka ma wuqar da aka yi yankan da ita, da ruwa sai ya zama jinin da yake xixxiga daga jikin dabbar bayan an yanka ta mai tsarki ne.

Mas'ala ta Sha Daya (11): Gyambubbuka da quraje idan jinin ya fito daga garesu najasa ne, amma idan yalon (fatsi-fatsin) ruwa ya fito, da ba a tabbatar cewa ya caquda da jini ba to mai tsarki ne.

Mas'ala ta sha (12): Kayan shafe-shafe da alkahol xin da ake amfani da su a cikin turarurrka da magunguna idan sun kasance masu bugarwa kuma asalinsu narkakku ne to najasa ne, idan kuma masu buguwar ne kuma asalinsu sandararru ne, daidai ne suna nan a hakan (wato a sandare) ko kuma sun canza zuwa narkakku (ruwa) to masu tsarki ne, sai dai bai halatta a sha su ba saboda suna bugarawa. Amma da ba a san

asalinsu ko haqiqarsu ba, shin sandararru ne ko kuma narkakku ne, to za a yi hukunci da tsarkinsu, duk da mun so kuma mun yi madalla da a nisance su, saboda zai iya yiwuwa daga baya a gane cewa asalinsu masu bugarwa ne, kuma narkakku (ruwa-ruwa).

Na shida da na Bakwai (6-7): Kare da Alade, hakama da gumin da yake fita daga-gare su – da kuma yawu da gashinsu – duka najasa ne: sai dai Kare da Aladen ruwa masu tsarki ne.

Na takwas (8): Giya da dukkanin wani abin sha mai bugurwa kamar wuski da banmi waxanda fasiqai suka saba shan su, su ma najasa ne.

Na tara (9) Kafiri wanda bai da addini, banda Bamajuse da Bayahude da kuma Banasare, najasa ne. Ihtiyaxi na wajibi, yin hukunci da najasarsu, amma Banasare, da Bahude, da kuma Bamajuse, waxannan an yi hukunci da tsarkin su.

Na goma (10): Gumin raqumi mai cin najasa-wato wanda ya saba cin kashin mutum- shi ma najasa ne.

Mas'ala ta Goma sha Uku (13): Duk abin da ya tava xaya daga cikin waxancan najasosi guda

goma idan (abin) ya kasance a jiqe to ya najastu, amma idan ya kasance busasshe to ba ya najastuwa, idan hanunka ya kasance a bushe sai ka tava wani guntun jini busasshe ko gaisawa (yin hannun) da kafiri (wanda yake najasa), amma hannun a bushe yake to hannun bai najastu ba, yana nan a tsarkake. Kamar yadda aka ce: “Busasshe a kan busasshe mai tsarki ne babu savani”.

Mas’ala ta Goma sha Huxu (14): Ruwa xan kaxan haka nan abu mai ruwa, (narkakken da ba sandararre ba) kamar miya da man shanu. Idan najasa ta faxa cikinsa komai qanqantarta dukkninsu sun najastu, amma idan abu ya kasance mai tauri ko sandararre kamar katako ko sandararren man shafawa ko cukui, to iya nahiyar da najasa ta faxa ne kawai ya najastu, da a ce xigon jini zai faxa akan cukui to ba ya najastar da dukansa, kaxai iya nahiya da jinin ya faxa ne kawai ya najastu, kuma zai iya yiwuwa a tsarkake shi a ci.

Mas’ala ta Goma sha Biyar (15): Kalolin mayuka da zuma da kayayyakin magunguna da makamantansu na daga kayayyakin buqatun da Fatocin da hukuncinsu ya riga ya gabata a

Mas'ala ta biyar (5) da ta shida (6)-waxanda ake kawowa daga qasashen kafirai-idan ba a tabbatar da najasar su ba to tsakakakku ne ya halasta a yi amfani da su wajen ci da shi.

Mas'ala ta Goma sha Shida (16): Bai halatta a sha ko a ci najasa ba, haka nan dukkanin wani abu da ya najastu da xaya daga cikin najasosi- da suka gabata-, a misali; da xigon jini zai faxa cikin wani abu da yake xauke da ruwa ko miya, bai halatta a sha ko a ci daga wannan abin ba, matuqar yana najasce.

Mas'ala ta Goma sha Bakwai (17): Bai halatta a najastar da masallatai ba, kai wajibi ne a tsarkake su, a wannan lokacin, da misali xigon jini zai faxa a ciki masallaci wajibi ne a tsarkake shi, da ace kai ba za ka iya hakan ba to ka sanar da wani domin ya tsarkake shi.

**Faxakarwa:**

Najasoshin nan guda goma-da aka ambata-ba zai yiyu a tsarkake su ba, ta kowane irin yanayi, amma abubuwan da ba waxannan ba, idan suka najastu, ta yiyu a iya tsarkake su, idan hannun ka ya najastu ko qasa ko tufafi ko makamancin su, za a iya tsarkake su, amma waxanne abubuwa ne ake iya tsarkake abubuwan da suka najastu da su, kuma ta yaya za a tsarkake su ko kuma ya ake tsarkakewar? Da sannu bayanin su zai zo a karatu na gaba.

## Masu Tsarkakewa

Masu Tsarkakewa: Wasu abubuwa ne da zai iya yiwuwa a tsarkake abubuwa masu najasa da su, kuma guda goma ne, kamar haka:-

Na xaya: Ruwa, zai yiwu a tsarkake abubuwan da suka najastu da xaya daga cikin najasosin da suka gabata ta hanyar zuba ruwa a kan su, amma kafin mu yi bayanin yadda ake tsarkakewa da ruwa za mu ambaci wata gabatarwa dangane da

kashe-kashen ruwa. Sannan daga baya mu yi bayanin yadda ake tsarkake ko wanne su da ruwa.

Don haka, mu ce: ruwa ya kasu kashi huxu

1) Ruwa mai gudu kamar kogi da na tafki da kuma ruwan idanuwa – da yake vuvvugowa – da ruwan shayarwa (na ban ruwa).

2) Ruwan sama a lokacin da yake sauka daga sama.

3) Ruwan Kur wanda faxinsa ya kai xani (kamun `yan yatsun hannu) 27 zuwa faxin kusurwoyi huxu ko murabba'i takwas wanda ya yi daidai kilo giram xari xaya (100) irin wanda ake tattara shi a tanki ko babban rami na gida.

4) Ruwa xan kaxan kamar wanda ake zubawa a buta ko bokiti da makamantan su, ta yadda ya zama ba su kai Kur ba (qasa da Kur).

Mas'ala ta sha takwas (18): Ruwan sama haka nan ruwan da yake gudu da kuma Kur, idan najasa ta faxa cikin su ba ya najasatuwa matuqar launinsa bai canza da launin najasar ba kuma xanxanon sa bai canza da xanxanon najasar ba sannan kuma qanshin sa bai canza ba daqanshin

ruwan najasar ba, idan jini ya faxa cikin tankin ruwa Kur, kuma bai canzo ba, to yana nan bisa tsarkinsa.

Amma da a ce jini da yawa zai faxa cikin sa ta yadda ruwan ya rine da launin ja ko kuma launin saya zama ruwan wardi to ya najastu, bai halatta a sha ko a yi alwala da shi ba, haka kuma da wata najasa kamar ta bawali za ta faxa cikin taikin ruwa sai ya zama yana warin bawali.

Mas'ala ta sha Tara (19): Ruwa tiyo wato ruwan famfo yana da hukuncin ruwan Kur, da ace ruwan tiyo zai zuba cikin bokiti ko kwano sai wani xigo na bawali ya faxa to bai najastu ba.

Mas'ala ta Ishirin (20): Ruwa xan kaxan yana najastuwa da najasa 'yar kaxan idan ta faxa cikinsa ko da ko xigon jini ne ko da launinsa bai canza ba.

Mas'ala ta Ishirin da Xaya (21): Ta yaya za mu tsarkake abubuwa da ruwa?

Amsa ita ce: Tsarkake abubuwa da ruwa yana tabbata ne ta bayanai masu zuwa filla-filla:-

1- Tufafi da Kot-kot da kafet da makamantansu,

ana tsarkake su da ruwa mai gudu ko ruwan Kur da kuma ruwan sama ta hanyar wankewa sau xaya, suna tsarkaka da an dulmiya su a cikin ruwan, kafet idan ruwan sama ya mamaye shi ko aka dulmiya shi a cikin tafki to ya tsarkaka, amma tsarkake su da ruwa xan kaxan yakan kasancewa ne ta hanyar wanke su sau biyu (2) da matse su bayan kowane wanki, idan sun najastu ne da bawali – banda bawali yaron da ake shayarwa- amma idan sun najastu ne da wanin bawali yana isarwa a wanke su sau xaya a matse, duka wannan bayan an gusar da najasar daga jikinsu.

2- Kwanukan cin abinci da na shan ruwa, ana tsakake su da ruwan sama ko ruwa mai gudu ko kuma ruwan Kur, ta hanyar wanke su sau xaya ne. Amma idan da ruwa kaxan ne sai a zuba ruwan a kan su bayan an gusar da najasar daga gare su, sai a cika su sannan a zubar da ruwa, sannan a sake cika su a zubur karo na biyu (2) a zubar a karo na uku (3) da haka ne suke tsarkaka.

3- Sauran buqatu kamar jiki da qasa da wasu kayayyakin daban kamar wuqa da abin da tsaftace01 haqora (Burosh) da makamantansu ana tsarkake su da ruwa mai gudu ko ruwa sama ko kuma ruwan Kur da wankewa sau xaya ne, amma

da sharaxin gusar da najasar daga garesu-kafin wankewa-. Amma tsarkake su da ruwa kaxan, idan sun najastu ne da bawali sai a wanke su sau biyu, idan kuma san najasta da wanin bawali ne sai a wanke su sau xaya, hakan yana isuwa ta hanyar zuba ruwan a kan ta bayan an gusar da najasar daga gare su.

Mas'ala ta 22:- Idan tufa ya najastu da abin da ba bawali ba kamar jini, sai kake son tsarkake shi da ruwa xan kaxan a bokiti, to zaka fara gusar da jinin da farko, sannan ka sanya tufar a cikin bokitin da babu komai na ruwa a cikinsa, sai ka zuba ruwan a cikin bokitin ta yadda zai sha kan tufafin, sai ka fitar da tufar ka matse ta, ka zubar da ruwan shi kenan tufar ta tsarkaka, haka nan shi ma bokitin.

Da a ce tufar ta najastu ne da bawali, to sai ka maimaita tsarkakewar sau biyu.

Mas'ala ta 23:- Idan yaron da ake shayarwa wanda ba ya cin abinci kuma namiji ya yi fitsari a tufafinsa ko makamancin haka, to tsarkake shi da ruwa kaxan sau xaya ya isar, amma ihitiyaxi na wajibi shi ne: a matse shi (bayan tsarkakewar).

Mai Tsarkakewa Na Biyu: Qasa, tana tsarkake

tafin qafa da kuma bayan takalmi idan suka najastu yayin da ake yin tafiya. Da mutum zai taka najasa, sai kuma ya yi tattaki a kan qasa wadda take mai tsarki kuma busasshiya har ainahin najasar ta gushe, to bayan takalmin ya tsarkaka. Haka nan da a ce babu takalmi a qafarsa kuma ya xora ta a kan najasa, tafin qafar na tsarkaka idan ya yi tattaki a kan qasa wacce take busasshiya tsarkakkiya.

Na Uku: Rana: Tana tsarkake qasa da dukkanin abubuwan da suke tabbatattu a kan qasar, kamar qofofi da itatuwa, idan suka kasance a jiqe, kuma nahiyar najasar ta bushe-bayan gusar da najasar-a sakamakon zafin ranar da ya dake su, daga nan sun tsakaka, babu buqatar sai an zuba ruwa a kansu.

Mas'ala ta 24:- Idan qasar da ta najastu ta kasance busasshiya, ta najastu da fitsari ne ko kuma waninsa, to ya isar a yayyafa mata ruwa, idan ta bushe dalilin zafin rana to ta tsarkaka ba sai an sake tsarkake ta da ruwa ba, amma da a ce ta bushe ne a dalilin kaxawar iska ko kuma gundarin najasar bai gushe ba, to tana nan da najasarta.

Na Huxu: Canzawar Najasa, abin da ake nufi a nan shi ne: Najasa na iya canzawa ta koma wani jiki daban, misali: Tururin da yake tasowa daga ruwan najasa ko kuma daga bawali mai tsarki ne, haka nan itacen da ya najastu yana tsarkaka idan aka qone shi, don haka, tokarsa mai tsarki ce.

Na Biyar: Samun Sauyi: Shi ne kamar giya ta juye ta zama kunu ko farau-rafau kamar yadda muka faxa a baya cewa, giya najasa ce. a lokacin yin kunu, tsumin kunun ya kan zama giya a farko sai ya zama ya najastu, sannan ya canza a hankali a hankali ya koma kunu to sai ya tsarkaka da wannan canzawar, wannan shi ne ma'anar sauyawar giya zuwa kunu.

Na Shida: Ciruwa: Misali jinin najasa ya ciratu zuwa qwari, misali jinin kare najasa ne shi kuma qwaro mai tsarki ne, to da a ce sauro zai zuqi jinin kare ya koma cikinsa, jinin zai zama wani vangare na jininsa, to ya tsarkaka, amma da za a kashe sauron a lokacin da yake zuqar jinin daga jikin Karen to jinin da aka ambata najasa ne.

Na Bakwai: Musulunci: Idan kafiri ya musulunta to ya tsarkaka, babu buqatar sai ya tsarkake jikinsa da ruwa ta hanyar wanka, sai dai

zai wanzu a matsayinsa na mai hadasi, inda zai buqatu zuwa wankan janabar da ta gabata. Misali: Idan ya zama mai janaba ko kuma matar da ta musulunta alhali tana jinin haila ce.

Na Takwas: Bibiya: Xan kafiri najasa ne kamar mahaifinsa a bisa ihtiyaxi na wajibi, amma da kafiri zai musulunta 'ya'yansa qanana sun bi shi a tsarki, sai dai a kwai wasu halaye daban na bibiya, sai ka yi nazarinsu a cikin manyan litattafai na fiqihu waxanda suka yi bayanai filla-filla.

Na Tara: Gushewar Ainahin Najasa: Shi ma yana wajabtar da tsarkakar abin da ya najastu, amma a bisa halaye guda biyu kawai:

(1) Jikin dabba, da kaza za ta ci abu mai najasa sai bakinta ya cakuxa da najasar, to ya tsarkaka da zarar najasar ta gushe daga bakinta, babu buqatar sai an tsarkake bakin da ruwa.

(2) Baxinin jikin mutum, da a ce jini ya fita daga bakin mutum ko kunnensa ko kuma hancinsa, to shi ma yana tsarkaka da zarar jinin ya gushe, babu buqatar cewa sai an tsarkake cikin kunnen ko hancin ko kuma cikin bakin da ruwa, amma da a ce levvbansa ne suka najastu to wajibi ne a tsarkake su da ruwa saboda suna daga zahirin jiki

ba baxini ba.

Na Goma: Vacewa: Da wani abokinka ko wani daga cikin ahalin gidanku wanda yake riqo da addini ne, kuma ya san cewa lalle wannan kwanon nasa mai najasa ne, bayan wani lokaci sai ka gan shi da shi yana shan wani abin sha a cikin wannan kwanon, to zaka yi hukunci da cewa lallai kwanon nan tsarkakke ne, ba ya wajaba a gareka ka tambaye shi cewa ya tsarkake kwanon ko kuwa? Saboda mumini ne kuma ba zai sha abin da yake najasa ba.

**Faxakarwa:**

Wajibi ne yayin yin fitsari ko biyan buqata, mutum ya faxaka; wato ya zavi wuri suturtacce kamar wajen da aka kawwame shi domin hakan, ba ya halatta ya yaye al'aurarsa a gaban mutane.

Mas'ala ta 25:- Tsarkake bigiren bawali da ruwa mai gudu ko da ruwan Kur sau xaya ne, amma sau biyu ne idan da ruwa kaxan ne, kamar idan ruwan buta ne. Amma kuma bigiren kashi -wurin tsarkake shi- yana isarwa ne a ci gaba da wanke shi sau xaya har zuwa gushewar najasar daga

bigiren, kuma ya halatta a gusar da najasar ta hanyar qyallaye guda uku ko tolfefa (tissue) har zuwa gushewar najasar, har sai wurin ya tsarkaka, ba tare da buqatar yin amfani da ruwa ba.

Mas'ala ta 26:- Ruwan da aka yi amfani da shi domin tsarkake wurin fitsari da kashi bayan an yi fitsari ko kashin mai tsarki ne, matuqar ba a ganin gutsattsarin najasar a cikinsa, ana kiran wannan ruwa (ruwa tsarkin hadasi).

Mas'ala ta 27: An fifita (mustahabbi ne) ga mazaje cewa su riqa kakkave mafitar fitsarinsu tare da matso abin da ya yi saura na daga fitsari domin tsarkake shi. Misali; ta hanyar matsa tushen al'aura har zuwa kan kaciyar. Bayan yin wannan, da a ce wani abu zai fito, wanda ake kokwanto a kan cewa shin fitsari ne ko waninsa ne to mai tsarki ne, ana kiran wannan aiki da (tsarkaka daga bawali).

## TAMBAYOYI

1) Abubuwan da suke tsarkake najasa guda nawa ne?

2) Faxi kashe-kashen ruwa.

3) Idan xigon fitsari ya faxa cikin tankin qarqashin ruwa ya najastu?

4) Idan xigon jini ya faxa cikin bokiti mai ruwa shin ya najastu?

5) Dardumar da ta najastu da fitsari ta yaya za a tsarkake ta da ruwan famfo?

6) Yaya ake tsarkake kwano mai najasa da ruwan kaxan?

7) Idan kana so ka tsarkake tufa da ruwan bokiti kaxan, kuma tufafin ya najastu ne da fitsari, yaya mutum zai yi?

8) Yaya zaka tsarkake bokitin da ya najastu da najasar da ba fitsari ba?

9) Idan qasa ta najastu da fitsari sai kake son tsarkake ta da ruwa kaxan, yana iya isarwa ruwan ya gudana a kanta sau xaya ko sau biyu?

10) A lokacin zafi raxaxin rana ya xaga sosai, to idan haskenta ya dira a kan qasa mai najasa har ta qeqasar da ita, shin ta tsarkaka ko kuwa tana buqatuwa zuwa tsarkake ta da ruwa?

11) John Yaro ne da mahaifinsa kafiri, sai kuma ya musulunta, to wace irin tsarkaka yaron ya yi daga cikin ababe masu tsarkakewa?

12) Idan haqorinka ya cire, sannan bakinka da levvanka suka cakuxa da jini, sai kuma jinin ya yanke, to wanne ne yake buqatuwa zuwa tsarkake shi da ruwa, wanne ne kuma yake tsarkaka da gushewar najasar?

13) Bayan an yi fitsari kuma yana son tsarkake bigiren da ruwan kumfa, sau nawa zai zuba ruwan? Idan kuma yana son tsarkake shi da ruwan buta ne sau nawa zai zuba ruwan?

## Alwala

## Yadda Ake Alwala

Alwala ita ce wanke fuska da hannaye da shafar kai da qafafuwa. Wajibi ne yin hakan ya zama da nufin alwala ba da nufin tsafta ba.

Abu na farko: Wanke fuska:

Iyakarta ta fuskacin tsawo shi ne daga matsirar gashin kai zuwa qarshen fuska, idan kana son ka san iyakarta, ta fuskacin faxi ka xora tafin hannunka a kan fuskar, sai ka wara yatsun ka iya nahiyar da ke tsakanin abin da gefen babban yatsanka da yatsanka na tsakiya suka kewaye nan ne ya wajaba ka wanke a fuskar ka,

Kuma ya wajaba –a yayin wanke fuska– ka fara daga sama zuwa qasa, a yayin da kake wankewar sai ka riqa sakko da hannun ka daga farkon fuskar zuwa qarshenta, kada ka yi akasin (savanin) haka, kuma kada ka wanke fuskar daga dama zuwa hagu ko kuma akasin haka.

## FAXAKARWA:

Ya kai mai girma mai karatu ko makaranciya, ta yiyu ka sha wahala wajen wanke fuska daga sama zuwa qasa a jere, (cuxawa bayan cuxawa), saboda mutum haqiqa mutum yakan buqatu ko ya manta ya motsa hannunsa savanin yadda aka faxa ko kuma dama da hagu, saboda haka a nan zan yi maka bayani da cewa ya isar maka tun farkon yin alwalar ka yi niyyar wankewar daga sama zuwa qasa, idan ka yi nufin hakan to wannan xan motsawar hannun naka zuwa wasu nahiyoyi ba ya cutarwa a wasu lokuta, kuma alwalarka ba ta vaci da hakan ba, sai ka koma ka shuxo hannun naka daga wancan wurin (farkon fuska) zuwa qarshen fuskarka cika alwalarka a bisa jerantawar.

Mas'ala ta 28:- Ba ya wajaba a wanke cikin levva da idanuwa, ko kuma cikin baki da hanci yayin alwala, ballantana ma wanke bayansu ya wadatar.

Mas'ala ta 29:- Duk abin da zai hana ruwa isa ga fata kamar kwantsar ido wacce ke fita yayin da ake bacci ko kwalli da wasu nau'o'in kayan kwalliya, ya wajaba a gusar da su yayin alwala, ta yadda ruwan zai isa dukkanin fuskar.



Mas'ala ta 30:- Idan gashin baki da gemu suka zama masu kauri ko duhu ya isar a wanke bayansu, ba ya wajaba a wanke qarqashinsu.

Na Biyu: Wanke

Hannaye:

Wanke hannaye daga gwiwar hannu zuwa gefen 'yan yatsu daga sama zuwa qasa, motsawa kaxan wadda ba wannan ba, ba ta cutarwa, idan har mai yin alwalar ba yana nufin alwala da wannan motsin ba, (wanda ba ya cikin alwala), kamar yadda muka bayyana a faxakarwar da ta gabata. Tilas ne a gabatar da wanke hannun dama kafin wanke hannun hagu.

Mas'ala ta 31:- Wasu daga cikin mutane sukan fara wanke tafukansu kafin su wanke fuska yayin da suka zo wanke hannayensu a alwala ba sa wanke tafin hannu, bisa tsammanin cewa wanke su da suka yi kafin alwala ya wadatar musu wajen wanke su yayin da suka zo yin alwalar, sai dai yin wananan tunanin bai inganta ba. Don haka yayin da ka zo wanke hannunka ka cika wankewar zuwa gefen `yan yatsunka.

Mas'ala ta 32:- Idan ya zama a kan hannayen mutum akwai dauxa ko wani abu da zai iya hana saduwar ruwa zuwa hannu, wajibi ne a gusar da shi.

Mas'ala ta 33:- Idan aka kammala wanke hannun hagu to ka kula da danshin cikin tafikanka, ka da ka cakuxa su da wani ruwan daban har sai ka shafi kanka da qafarka ta dama, sai kuma ka shafi qafarka ta hagu da danshin cikin tafin hannun hagu kamar yadda da sannu za mu yi bayaninsa (a nan gaba).

Na Uku: Shi ne shafar gaban kai da cikin hannun dama:

A bisa ihtiyaxi na wajibi, ya isar a shafi magabacin saman kai, da cikin tafin hannu, ta vangaren tsawo; daga qoqoluwar kai zuwa mafarar gashin kai. Faxi kuma; shi ne abin da ya yi daidai da faxin goshi, kuma ba wajibi ba ne a shafe shi duka. Ballantana ma! yana isarwa ka shafi wani vangare, komai qanqantarsa ko da gwargwadon xan yatsa ne.

Kuma wajibi ne abin da za a shafa ya zama gashin da yake a kwance a magabacin kai, amma gashin da ya yi tsawo wanda ya miqe ya fita

wajen magabacin kai -wanda yake reto- shafa a kansa ba ta isarwa, kamar yadda, da mace za ta tattara gashinta wanda ya yi tsawo a kanta ta shafe shi, haka ma ba ya isarwa.




Mas'ala ta 34:- Yayin shafar kai, ka xora hannunka ko 'yan yatsunka a tsakiyar kai, sai ka motsa su zuwa daura da fuska ko yaya ne, ba tare da la'akari da yadda ka saita tafin hannun ka ba, gaba a baya ka xora shi, ko a kaikaice, ko a shimfixe.

Ka faxaka, kada ka sauko da hannunka zuwa fuska har danshin hannunka ya cakuxa da danshin fuskarka. Lalle ka kula da haqiqanin danshin da ke hannun har sai ka shafi qafarka ta dama da shi.

Mas'ala ta 35:- Kada gashin kanka ya zama mai danshi kafin shafar kai, maimakon haka ya zama busasshe yayin shafar, amma 'yar qaramar lema ba ta cutarwa.

Na Huxu: Shafar bayan qafafu:

Iyakacinsa ta fuskacin tsawo daga gefen 'yan

yatsu ne zuwa mararrabar qafa, ta fuskacin faxi kuma shi ne, ka shafi wani abu komai qanqantarsa ko da gwargwadon kan xan yatsa ne, amma an fifita a yi shafar da gaba xayan tafin hannu, sai ka shafi bayan qafar dama da farko, da danshin cikin tafin hannun dama, sannan ka shafi bayan qafar hagu da danshin cikin tafin hannun hagu.

Mas'ala ta 36:- Wajibi ne ka da ya zama akwai dauxa a kan saman fata wadda za ta hana saduwa ko isuwar ruwa zuwa fata, ko kuma gashin da ya tsiro a kan qafar ya zama zai iya hana ruwa isuwa zuwa gareta.

Mas'ala ta 37:- Ka kula, kada saman qafar ya zama da lema yayin shafa, ka tabbatar ka busar da shi kafin shafar.

Mas'ala ta 38:- Ya isar ga hannun da a ke shafar kai da qafa da shi, ya zama mai danshi yayin shafar, ba wajibi ba ne sai an ga danshi a saman qafar bayan an yi shafar ba.

## Fasali Na biyu

## Sharuxxan Alwala

Wasu abubuwa ne waxanda idan suka tabbata sai alwala ta inganta, idan kuma aka rasa xaya daga cikinsu sai alwala ta zama ta vaci,waxannan abubuwa suna da yawa. Amma manya daga cikinsu guda shida ne:

**Na xaya:** Ruwan ya zama mai tsarki, ba wanda ya najastu da xaya daga cikin najasosin nan guda goma ba.

**Na biyu:** Kada ruwan ya zama na qwace.

**Na uku:** Gavvan alwalar su zama masu tsarki, domin kada ruwan da za a yi alwalar ya najastu da ita, sai alwalar ta qi tabbata.

**Na huxu:** Kada wajen da ake yin alwala a cikinsa ya zama na qwace, ta yadda niyyar neman kusancin da Allah ba za ta karvu ba.



**Na biyar:** Niyyar neman kusanci da Allah, da ma'anar alwalar ta zamo domin biyayya

ga Allah maxaukaki, ba wai domin wata manufa ba.

Ka faxaka ya kai mai karatu ko makaranciya don kada ka yi alwala domin jin tsoron 'yan gidanka, irin wannan alwalar ba ta inganta ba. Abin da ya zama lalle shi ne jin tsoronka ga Allah ya zama shi ne a gaba, saboda azabar Allah da wutar jahannamansa ita ta fi tsanani sosai a kan uqubar danginka. Yin alwalarka ta zama saboda biyayya ga ubangijinka, ka kuma nisanci sava masa har sai Allah ya karva maka.

**Na shida:** Bibiya-Bi daki-daki-, wato; kada mai alwala ya samar da wata tsayawa ta wani lokaci a tsakanin wanke gavovinsa, misali ya wanke hannunsa, sai kuma ya shagaltu da wani aiki ko wasa har fuskarsa da hannunsa su bushe, sannan ya cika alwalarsa, irin wannan alwala ba ta inganta ba.





## Fasali Na Uku

## Masu Vata Alwala

Manya-manya daga cikin guda huxu ne: Bawali, da gayaxi, da tusa, da kuma bacci.

Duk wanda ya zama yana da alwala sai xaya daga cinkin waxannan al'amura ya zo masa to alwalarsa ta vaci, wajibi ne a gareshi ya sake wata alwalar, misali saboda salla.

Mas'ala ta 39:- Idan tun farko mutum bai san cewa yana da alwala ba to wajibi ne a gareshi ya yi alwala saboda salla a misali.

Mas'ala ta 40:- Idan ya zamana mutum yana da alwala sai ya yi shakkun shin xaya daga cikin waxancan al'amura ya zo masa ko kuwa, to alwalarsa tana nan ba ta vaci ba, ba ya wajaba a gareshi ya sake wata alwalar ba.

Mas'ala ta 41:- Mustahabbi ne mutum ya kasance a cikin alwala ko da yaushe ko da kuwa ba lokacin salla ba ne, haka ma yin alwala kafin ya yi bacci. Ya zo a cikin hadisi daga Imam Sadiq amincin Allah ya tabbata a gareshi ya ce: "Duk

wanda ya wayi gari a kan tsarki kamar ya raya dare ne".

Mas'ala ta 42:- Akwai wasu abubuwa da yi musu alwala bai zama wajibai ba, amma an so a yi riqo da su saboda lada. Kamar kuskurar baki da shaqa ruwa sau uku kafin a fara wanke fuska, da kuma yin bisimilla lokacin yin alwala.

Idan mai alwala ya wanke fuskarsa sai ya faxi abin da Imam Ali amincin Allah ya tabbata a gareshi, yake faxi: Ya ubangiji ka haskaka fuskata a ranar da fusaku suke zama baqaqe, kada ka baqanta fuskata a ranar da fusaku suke zama farare. Idan ya wanke hannunsa na dama yana cewa: Ya ubangiji ka ba ni litattafina a hannun dama, takardar tabbata a aljanna kuma a hannun haguna, ka yi mini hisabi mai sauqi. Yayin da yake wanke hannunsa na hagu kuma yana cewa: Ya ubangiji kada ka ba ni littafina a hannun hagu, kada ka sanya su ababan yin ququmi ta wuyana (soko su ta cikin wuya su fito ta bayan wuyan) ina neman tsarinka daga yanyankewar nan ta wuta. A yayin da yake shafi kansa kuma sai ya ce: ya Allah ka lulluve ni da rahamarka da albarkarka da afuwarka. Haka kuma idan ya shafi qafarsa yana cewa: Ya ubangiji ka tabbatar da ni a kan siraxi a

ranar da dugadugai suke zamewa, ka sanya kai da komowa ta a cikin abin da zan sami yardar ka.

Mas'ala ta 43:- Ba ya halatta ga wanda ba shi da alwala ya tava rubutun Kur'ani, a bisa ihtiyaxi na wajibi, ya kuma nisanci tava ayoyin Kur'ani na cikin wasu littattafan daban, kamar yadda ba ya halatta a tava sunayen na lafazin jalala wato (Allah) da sauran sunayen Allah na musamman. Misalin Arrahman, Albari, Alquddusu da makamantansu.

## Taimama

### Sababan Yin Taimama

Taimama ta wajaba ga wanda ba zai iya yin alwala da ruwa, saboda wani dalili na daga cikin dalilai, manya daga cikin guda uku ne:

Na Xaya: Rashin samun ruwa ga mutum, saboda kada ya bar salla sai ya yi taimama ya yi salla, kuma sallar tasa ta inganta matuqar bai sami ruwa a tsawon lokacin sallar ba.

Na Biyu: Idan yin amfani da ruwan zai cutar da mutum, domin Allah maxaukaki ba ya nufin ya cutar da mutum, sai ya sanya wa marasa lafiyan da ruwa zai iya cutar da su musaya mai sauqi, shi ne taimama, idan ruwa zai cutar da mutum lokacin salla sai ya yi taimama ya yi salla, kuma sallar ta inganta.

Na Uku: Idan ya zamana mutum yana da ruwa kaxan, ta yadda idan ya yi amfani da shi akwai jin tsoron qishirwa mai tsanani ta same shi, ta yiwu ma ya halaka ko kuma ya galabaita a sakamakon

qishirwar, lalle shi Allah mai tsarki bai yarda mumini ya cutu ba, sai ya sanya taimama ta zama canji ga alwala.

Haka nan idan ka ga wani mumini qishirwa ta yi tasiri a kansa, to kada ka yi alwala da ruwa xan kaxan da yake a wajenka, maimakon haka ka ba shi ya sha, domin kare mumini daga cutuwa ya fi mihimmanci, domin shi muminin yana da girma a wajen Allah.

Mas'ala ta 34:- Idan lokaci ya yi qunci domin yin alwala da salla, kamar idan ka makara wajen tashi daga bacci lokacin alfijir zuwa fitowar rana, ta yadda ka sami masaniyar cewa idan har sai ka yi alwala sannan ka yi salla to rana za ta fito, idan zai yiwu a gareka ka gaugauta yin taimama ka yi salla kafin ranar ta fito, to an fifita yin gaugawar yin taimamar da salla, sai dai ya wajaba a gareka ka yi alwala da ruwa ka rama sallar daga baya.

## Abubuwan Da Ake Taimama Da Su

Tabbas mai karatu zai iya tambaya yana mai cewa: A kan me ake yin taimama?

Amsa ita ce: Yin taimama ya halatta a kan qasa wacce take busasshiya da bisa xabi'a (kamar dai yadda qasa take), kamar turvaya da yashi da tsakuwoyi da dutse da kuma marmara. kamar yadda ya halatta a yi a kan misalin fulasta da siminti da jan gargari (farar kasa) da jan bulo da makamantansu ba.

Mas'ala ta 45:- Bai halatta ba a yi taimama a kan gilashi da tsirrai da toka da qarfe da kuma kan tufafi

Mas'ala ta 46:- Bai halatta ba a yi taimama a kan qasa wadda take ba busasshiya ba, kamar yadda yake ba ya halatta a yi a kan qasa wacce take ta qwace, wadda masu ita ba su yarda a yi taimama a kanta ba, matuqar mai taimamar yana da masaniya da haramcin yin amfani ga abin qwacen, wanda ba a samun ladan niyyar neman kusanci zuwa ga Allah maxaukaki, don haka taimamarsa ba ta inganta ba.

## Yadda Ake Taimama

Ina fatan faxakar da masoyana mumini da mumina masu girma sanin yadda ake yin taimama, saboda kada ku auka cikin kuskure. Ga yadda ake yin ta, kamar haka:

Ka bugi qasa (turvaya) da cikin tafukanka na hannu bugu xaya, sannan an fifita ka kakkave su ta hanyar gwara xaya da xayan, sai ka shafi gaba xayan goshin ka da gaba xayan kunduquqi (wato qashin kumatu) daga matsirar gashi zuwa qarshen kunduquqi, da kuma gaba xayan gira da gaba xayan gefen hanncin na sama, gaba xaya za ka shafi wannan bisa jerantawa daga sama zuwa qasa. Kuma kada ka motsa hannayenka dama da hagu daga sama zuwa qasa har ka game dukkanin nahiyar biki xaya.

Sannan sai ka shafi gaba xayan tafinka na dama, daga wuyan hannu zuwa gefen 'yan yatsu da cikin tafin hannunka na hagu, sai kuma ka shafi gaba xayan tafin hannunka na hagu shi ma daga wuyan hannu zuwa gefen 'yan yatsu da cikin tafinka na hannun dama. Kuma shafar da muka ambata ta zamo a bisa jerantawa, ba ka riqa motsa hannunka dama da hagu ba. Wannan shi ne yadda ake yin

taimama a bisa wajibi.

Amma an fifita a daki qasar duka na biyu, sai a kakkave hannayen, sannan a shafi bayan hannun dama sannan na hagu, da yanayin da ya gabata a baya.

Mas'ala ta 47:- Wajibi ne yin taimama ya zama da nufin neman kusanci zuwa Allah, sannan ya wajaba a gusar da dauxa da cire zobe da duk wani abu da zai hana a yi shar a fatar hannun.

Mas'ala ta 48:- Duk wanda taimama ta wajaba a gareshi a sakamakon gazawarsa ga yin alwala (da ruwa) to bai halatta ba gareshi ya yi taimamar kafin shigar lokacin salla a bisa ihtiyaxi na wajibi, a maimakon haka; ya saurara har lokacin sallar ya shiga sai ya yi taimamar saboda ita.

Da yin alwalar zai zama yana cutar da kai, sai ka zo kana son ka yi taimama saboda sallar Azahar misali, to kada ka yi taimamar kafin lokacin Azahar xin. Lalle ka jinkirta har ya zama lokacin Azahar xin ya shiga, sannan ka yi taimama.

## FAXAKARWA:

Idan wani vangare daga wuraren alwala a karye yake ko kuma yana da rauni, ba kuma zai yiwu a tsarkake shi ba, to akwai wasu hukunce-hukunce filla-filla da aka ambace su a cikin manya-manyan littattafan fiqihu yayin alwala.











TAMBYOYI

1- Shin ya halatta ka wanke fuskarka da hannayenka daga dama zuwa hagu, ba wai daga sama zuwa qasa ba?

2- Idan mace ta tattara gashinta wuri guda, shin ya halatta gareta ta yi shafa a kansa a alwala?

3- Ka qirga adadin sharaxan inganci na alwala.

4- Shin ka yi alwala a gaban wani mutum mai koyarwa, ta yadda ya bayyana maka kuskuren da ka kan rafkana da su?

5- Mene ne abubuwan da suke vata alwala?

6- Idan ka yi alwala da safe ko kuma da Azahar ba tare da ka san wani abu daga cikin abubuwan da suke vata alwala ya zo maka ba ko kuma a'a, to shin alwalarka da ta gabata ta isar maka? Ko kuwa wajibi ne a kanka ka sake sabuwar alwala?

7- Waxanne abubuwa ne suke wajabtar da alwala?

8- Shin ya halatta a yi alwala a kan siminti?

9- Shin alwala ta inganta ba tare da an kakkave hannaye ba?

10- Wace nahiya ce ya wajaba a shafa game da fuska yayin taimama.

**Janaba**

Janaba tana tabbata da xayan abubuwa guda biyu:

1- Fitar maniyyi ko da kuwa ba tare da jima'i ba, kuma ihtiyaxi na wajibi, ita ma mace janaba na tabbata a kanta ta hanyar yin inzali (fitar maniyyi), kuma wannan na wajabta mata ta haxa tsakanin wanka da da alwala bisa ihtiyaxi. (na wajibi).

2- Yin jima'i (tarawa) ko saduwa tsakanin namiji da mace.

Mas'aloli:

Mas'ala ta 21: Dukkanin abin da bai halatta ga maras alwala ba, ba ya halatta ga mai janaba.

Mas'ala ta 22: Azumi ba ya halatta a gareshi. (Ka yi muraja'ar babin azumi).

Mas'ala ta 23: Ya haramta ga mai janaba dukkanin abin da ya haramta ga maras alwala.

Mas'ala ta 24: Ya haramta a gareshi ya shiga masallaci mai alfarma, ko kuma masallacin

Annabi maxaukaki, koda kuma wucewa ta cikinsa ne.

Mas'ala ta 25: ya haramta a gareshi ya zauna a cikin masalatai kuma ihtiyaxi na wajibi kada ya zauna a hubbarori ma'asumai masu tsarki, amma ya halatta ya wuce ta cikinsu daga wata qofa zuwa wata.

Mas'ala ta 26: ya haramta a gareshi ya karanta ayar sujada daga surar aza'im guda huxu, su ne (alif lammim assajda) da (hammim assajda) da (najami) da kuma (alaqi).

**Wanka**

Wanka ya wajaba ga mai janaba, namiji ne shi ko mace, haka ma mai haila,-akwai wasu huhunce-hukunce da aka ambata dalla-dalla a cikin manyan littattafan fiqihu.

Wajiban Wanka:-

Abubuwa masu zuwa sun wajaba a cikin wanka:

1- Niyya. 2-Yi da kai. 3-Ruwa ya tava fatar jiki. 4-Tsarkin ruwa. 5-halaccin sa. 6-kasantuwar sa muxlaqi, kamar yadda bayaninsa ya gabata a cikin alwala.

Yadda ake yin Wanka:-

Ya wajaba a yayin wanka a jiqa dukkanin jiki da ruwa ta yadda ruwa zai kai zuwa gareshi, ko da kuwa kaxan kaxan ne, tamkar man shafawa. Yin sa ta wani ayyanannen yanayi ba wajibi ba ne, illa iyaka bai halatta a gabatar da wanke jiki kafin wanke kai ba.

Mafifici a gareshi shi ne: Ya yi wankan irtimasi ta hanyar nutsar da jiki baki xayansa a ruwa. Ko kuma wankan tartibi ta hanyar wanke dukkanin

kai da wuya sannan vangaren jiki na dama gaba xayansa sannan vangaren hagu shi ma haka.

Mas'ala ta 27: Wankan janaba na isarwa ga alwala, haka ma dukkanin wanka da yake na shari'a ne, wajibi ne shi ko mustahabbi, misalin sallar juma'a kafin sallar azahar.

Mas'ala ta 28: Idan wanka masu yawa suka taru a kan mutum, wanka xaya ya isar tare da yin niyyar haxawa ko yin niyyar sshai daga cikin su kamar wankan janaba.

Mas'ala ta 29: Ba'a sharxanta bibiya ba a cikin wankan.

Mas'ala ta 30: Idan mutum ya yi hadasi qarami a lokacin da yake cikin yin wanka, sai ya ci gaba da wankan kuma ya isar masa, amma mafifici ya sake shi, kuma babu makawa da ya yi alwala a tare da shi.

Mas'ala ta 31: Idan ya yi kokwanto a kan janaba sai ya yi gini a kan rashinta, idan kuma ya yi yaqini sai ya yi shakka a kan cewa shi ya yi wanka ko kuwa, sai ya yi gini a kan rashin yin wankan, sai dai in shakku ya canza ya zama waswasi , haqiqa a wannan lokacin ba zai kula da

ita ba kuma zai yi gini a kan tsarki.

Mas'ala ta 32: An so ga namiji ya yi istibra'in maniyyi ta hanyar yin bawali kafin wankan janaba, amfaninsa shi ne: ruwa mai kamaceceniyan da yake fita bayan bawali ba za a yi masa hukuncin maniyyi ba a shari'ance, amma da wannan ruwan da aka ambata zai fita kafin bawali, to ya zama wajibi a tabbatar masa da hukuncin maniyyi.

**Jinin Haila**

Ma'anarsa: Shi ne jini da mace ta saba gani, wanda yake fita daga mahaifa bayan da mace ta cika shekaru tara na musulumci, kafin shekarun yanke qauna, shekara sittin (60) ga baquraishiya wacce ba haka ba shekaru hamsin (50).

Siffar sa da aka sani:

Ja ne makusanci zuwa baqi, mai xumi yana fita da izar juna da quna.

Iya kacin sa:

Mafi qarancin kwanakinsa kwana uku ne, koda kuwa sun warwatsu a cikin kwanaki goma. Bayannin hukunce-hukuncenta da abubuwan da mai haila ta kevanta da su, an ambace su a cikin manyan litattafanfn fiqihu, sai ka koma zuwa gare su.

## Salla

Salla tana daga cikin mafi girman wajibi da yake kan mutum, wadda ya wajaba ya yi riqo da ita, kuma an fifita yin ta a farkon lokacinta da dukkanin sharuxanta, kuma ya yi ta yana mai tsoron Allah.

Ya zo a cikin hadisi cewa: "Salla ita ce ginshiqin addini, idan aka karve ta an karvi abin da ba ita ba, idan kuma aka mayar wa mutum ita, za a dawo masa da dukkan abin da ba ita ba". Wato idan har ba a karve ta daga mutum ba sakamakon rashin cikar wani sashi na sharuxanta, ko kuma yake wulaqanta ta, to ba za a karvi sauran dukkanin ayyukan ibadarsa ba. Amma idan ya bayar da ita bisa ingantaccen tsarinta kuma yana mai neman kuasnci zuwa ga Allah, to za a karvi ayyukansa kuma ladansa zai zamo mai yawa.

A cikin wani hadisi da aka karvo daga manzon Allah amincin Allah ya tabbata agareshi da alayen sa: “Ku sani cewa; Allah maxaukaki ya rantse da buwayarsa, cewa tabbas ba zai tavar da masu yin salla da masu yin sujjada, kuma ba zai tsorata su

da wuta ba, a ranar da mutane zasu tsaya ga ubangijin talikai”.

Har wala yau ya zo a hadisi daga Imam Sadiq amincin Allah ya qara tabbata a gareshi ya ce: Kada ka riqa qin kula da sallarka, domin Annabi amincin Allah ya qara tabbata a gareshi da 'ya'yan gidansa yana faxa yayin da zai rasu, cewa: Duk wanda yake wulaqanta sallarsa ba ya tare da ni, wallahi ba zai tava gangarawa tafkina ba.

Daga Imam Sadiq amincin Allah ya tabbata a gareshi ya faxa a lokacin da wafati ya zo masa: Lallai cetonmu ba zai sami wanda yake sako-sako da salla ba.

Ka yi tunani ya kai mai girma mai karatu da mai girma makaranciya da cewa, idan har Allah (s.w.t) ba ya karvar ayyukaumu, kuma Annabin Allah (s.a.w) da Imamai (a.s) masu tsarki za su qi cetonmu ranar qiyama, to kuma wurin wa zamu jingina? wane ne kuma zai tseratar da mu?.

Shin zamu koma zuwa ga shaixan ne, da jama'arsa ashararai waxanda su ma suna cikin mafi tsananin azaba, harasan wuta da qunar na tsattsaga ko sassara fuskokin (kamar yadda saran takobi ya ke)? Sannan shin zamu yarda da

kawukanmu a matsayin musulmai na haqiqa, alhali an jefa mu cikin rundunar iblis, bayan da Allah maxaukaki ya kore mu, annabinmu amincin Allah ya tabbata a gareshi da imamanmu amincin Allah ya tabbata a gare su sun qi karvar mu?

Idan har wannan ce makomar wanda yake wulaqanta salla, to kuma ina ga mai barin yin ta?! Kuma ya azabarsa zata kasance!? Idan haka ne mu yi taimakekeniya tare, saboda mu kuvuta daga fushin Allah da azabarsa, domin mu rabauta da ceton Annabi tsira da amincin Allah su qara tabbata a gareshi, da imamai masu tsarki, mu sha daga tafkin nan na ma'akin Allah (s.a.w) ranar qishirwar nan babba.

Mataki na farko mu dogara ga Allah, kuma mu yi riqo tare da himmantuwa da sallarmu, mu riqa yin ta a farkon lokacinta, kada mu riqa la'akari da zantukan asharararai waxanda ba sa bayar da salla, kuma suna aiwatar da dukkanin munanan ayyuka haramtattu.

Mu lura sosai da bambancin da ke tsakanin masu yin salla da waxanda ba sa yi, ranar alqiyama, a cikin abin da Allah ya hakaito a cikin Kur'ani mai girma {Su ne waxannan da suke masu

kiyayewa ga sallarsu * waxannan ne waxanda suke tabbatuwa a cikin aljannatai ababan girmamawa}. Ma'arij (34-35).

"A cikin aljannatai `yan aljannan suna tambayar junanan su * Game da masu laifi (waxanda suka yi aikin banza) * (sannan sai su tambayi `yanwuta cewa:-) Mene ne ya shigar da ku cikin-wutar – Saqara * Sai su ce: Ba mu kasance daga cikin masu salla ba". Mudassir, aya ta: (40-43).

Kuma kana da zavi tsakanin ka zama daga cikin masu kiyaye salla ko kuma wasunsu, wato aljanna ko kuma wutar saqara, wacce ke jiran ma'abotanta.

**Lokutan Salla Da Adadinta**

A kowace rana ya wajaba a yi salloli biyar, su ne kamar haka:

(1) Sallar alfijir (Asuba): Raka'a biyu ce, lokacinta kuma na farawa daga hudowar alfijir, wanda shi ne farkon hasken da yake fitowa a sasannin gabas, har zuwa hudowar rana.

(2 – 3) Sallolin Azahar da La'asar, raka'o'i huxu ne, kuma lokacinsu yana farawa ne daga rabin rana na biyu, wanda ake kira da karkatar rana, (wato zawali), har zuwa lokacin da rana za ta faxi, amma ana gabatar da sallar Azahar a kan sallar La'asar.

Idan mun qaddara cewa hudowar rana yana kamawa ne daga qarfe bakwai (7) na safe a misali, faxuwarta kuma yana kamawa ne a qarfe shida (6) na yamma, to tsawon ranar yakan zama awa goma sha xaya 11 kuma karkatar rana zai zama bayan qarewar kaso na farko daga wuni, wato: (12 – 30) na Azahar.

(4)Sallar Magariba: Raka'a uku ce.

(5) Sallar Isha'i: Ita kuma raka'a huxu ce, lokacinsu yana farawa ne daga faxuwar kaskon rana,-amma an fifita a jinkirta yin ta zuwa vacewar jan nan da yake bayyana a vangaren gabas,-har zuwa rabin dare. Ana gabatar da sallar Magariba a kan sallar Isha'i, idan ya faru cewa mutum ya manta bai yi su ba, (a lokacinsu) to ya sallace su kfin fitowar alfijir.

Rabin dare shi ne rabin lokaci daga zarar rana ta faxi zuwa fitowar alfijir.

## Tufafin Mai Salla

Ba ya halatta ga mutum ya yi salla tsirara ko da kuwa shi kaxai ne a cikin xaki, ta yadda wani ba zai gan shi ba. Ballantana ma! Wajibi ne ga mazaje su suturce al'aurarsu; Mace kuwa ya wajaba ta suturce dukkan jikinta a yayin salla, ban da fuskarta da tafukan hannayenta. Amma rashin suturce dugaduganta a yayin salla ya halatta, idan har ba bu wani namiji muharraminta da zai gan ta. Kuma ya wajaba tufafin mai salla ya cika sharuxa guda shiga:

Abu na farko: Ya zama abin da mutum zai sa a yayin sallar na halal ne, wato ba na qwace ba ne. Idan mace ta san cewa abaya ko tufafin da za ta saka na qwace ne, ko kuma namiji ya san cewa abin da zai saka na qwace ne, to sallarsu ta vaci, sai dai idan mutum bai san cewa abin da ya suturta da shi a cikin sallarsa na qwace ne ba, amma sai ya san hakan bayan da ya gama sallar, to sallarsa da ta gabata ta inganta, amma ba ya halatta ya sake saka shi, saboda sallolin na gaba ba.

Abu na biyu: Kada tufafin mai salla ya zama

daga fatar mushe, daga cikin ire-iren fatun da ake zuwa da su daga waje ko kuma qasashen da ba na musulmi ba, har da irin fatar agogo idan ta kasance daga fatar dabba ne to salla ba ta inganta da ita. Haka nan maxaurin wando (belt) na fatu, da sauran yanke-yanken qananan fatu da ake xinke wasu tufafi da su.

Abu na uku: Kada fatar ta kasance daga vangaren dabbobin da aka haramta cin namansu, na daga fatunsu da gashinsu da makamantansu. Ba ya halatta a yi salla a cikin tufa ko hular da suke daga fatar dila ga misali, kai har ma abin da ya xamfaru jikinka ko tufafinka na daga gashin mage, a bisa ihtiyaxi na wajibi a gusar da su yayin salla.

Mas'ala ta 49:- Idan akwai fatar da ba a san cewa ta asali ba ce ko kuwa ta qirqira ce, to salla ta halatta a cikinta, saboda ba ka da masaniyar cewa ta fatar dabba ce.

Abu na huxu da na biyar: Ba ya halatta ga mazaje su sanya tufafin zinare da na alhariri, a yayin yin salla, amma ya halatta ga mata.

Abu na shida: Tufafin mai salla ya zama mai tsarki, bai halatta a yi salla da tufafi mai najasa ba,

haka nan jiki bai halatta ya zama mai najasa ba, amma a wannan qa'idar an togace wasu halaye da ya halatta a cikin su a yi salla da najasa, manya daga cikinsu guda uku ne

1. Jinin ciwo da na gyambo wanda ya cakuxa da jini a cikin jiki da tufafi, haka nan maganin da aka xora a kan ciwon, to shi irin wannan jinin matuqar ciwon bai warke ba salla ta halatta tare da shi, ba wajibi ba ne sai an gusar da shi ko kuma sai an tsarkake shi.

2. Jinin da yake xan kaxan da yake a kan tufafi, amma banda jinin biqi da na haila a bisa ihtiyaxi na wajibi, idan har bai wuce xige-xige santi mita biyu da milmita uku ba, amma jini xan kaxan da yake a kan jiki wanda ba na ciwo ko na gyambo ba to a bisa ihtiyaxi na wajibi a tsarkake shi.

3. Tufafi da sauran abubuwa qanana da ake sawa wanda ba za a iya suturce al'aura da su ba, kamar safa da zobe, ya halatta a yi salla da su ko da kuwa suna da najasa. Amma yin sallar bai halatta da su ba idan an yi su ne daga mushe ko kuma wani abu wanda najasa ne ainihinsa, kamar alade, a bisa ihtiyaxi na wajibi rashin yin afuwa ga abin da yake daga abu mai najasar da bai halatta a ci

namansa ba.

Bai halatta a yi salla a wuri da farfajiyar da suke na qwace ba, idan har mai sallar ya faxaka da haramcin hakan, saboda salla ibada ce da aka sharaxanta neman kusancin Allah maxaukaki a cikinta, neman kusanci kuwa ba ya yiwuwa ta hanyar yin amfani da abin qwace.

Mas'ala ta 50:- Wanda aka tsare a wuri na qwace ya halatta ya yi salla a wannan wurin, idan har ba zai zama sanadin lalacewar wurin ba.

Mas'ala ta 51:- Wuraren da suka shafi al'umma kamar masallatai da husainiyyoyi da wasu filaye da lambuna na jama'a, idan wani mutum ya gabaci zama ko salla a wurin to bai halatta a kawar da shi daga wurin ba ta qarfin tsiya, sai dai idan ya bar wuri, amma idan ya saka alama ko shimfixa ko kuma darduma a wurin har tsawon wani lokaci, to ya halatta ga waninsa ya zauna ko ya yi salla a wurin, sai dai ya kiyaye da kada ya yi amfani da shimfixar ko dardumar.

Mas'ala ta 52:- Ba ya halatta a shagaltar da hanyoyin musulmi, waxanda aka tanada saboda wucewa, da wani abu daban ba wannan ba. Kamar yin salla da saye da sayarwa da makarantunsu

idan har hakan ya kai ga cunkoson masu wucewa tare da cutar da su.

Mas'ala ta 53:- Sallar namiji da mace ta halatta a wurare gab-da-gab, shin namijin shi ne ya gabata ko kuwa macen ita ce ta gabata, ko kuma suna daura da juna. Amma an fi son namijin ya gabata, idan har babu hijabi a tsakaninsu, ko kuma tsakaninsu yana da nisa.

Mas'ala ta 54:- Bai halatta ba ga mai yin salla a makwancin Annabi (s.a.w) da na imamai (a.s) ya gabaci kabarinsu, ta yadda za su zama a bayansa.

**Alqibla**

Wajibi ne a fuskanci alqibla mai girma, saboda ita ce alqiblar musulmi, haka nan (a fuskanci) abin da ke samanta na sararin samaniya dangane da waxanda suka hau jirgi.

Mas'ala ta 55:- Idan mutum ya sami kansa a wani wuri wanda bai san alqibla ba, zai iya yiwuwa ya dogara da shaidar adalai biyu game da alqibla, kamar yadda ya halatta a gareshi ya yi salla yana mai kallom alqiblar da ya sami musulmai suna fuskanta a wannan yankin, ko kuma suka gina harabar masallacin (musamman alamar wurin da liman ke fuskanta).

## Yadda Ake Yin Salla

### Kiran Salla Da Iqama

Mustahabbi ne a yi kiran salla da iqama, a sallolin farilla da ake yi guda biyar na yau da kullun.

Mas'ala ta 56:- Kiran salla da iqama sau xaya ya isar a sallar jam'i, daidai ne mai kiran sallar ko wanda ya tsayar da iqamar shi ne liman ko kuma xaya ne daga cikin muminai (masallatan).

Mas'ala ta 57:- Ya cancanta ga mace ta isu ga barin yin kiran salla ta hanyar yin kabbara da shaidawar nan guda biyu – wato Allahu akbar – Ashhadu an la'ilaha illallahu – Ashhadu anna Muhammadan rasulullahi. Kai za ta iya isuwa da shaidawar guda biyu kawai, kamar yadda za ta iya isuwa ga iqama ta hanyar yin kabbara da kuma shahadatu an la'ilaha illallahu wa ashhadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluhu. Idan kuma ta ji kiran salla to tana iya isuwa a maimakon iqama, da shahadar nan biyu.

## Yadda Ake Kiran Salla

Yin kiran salla yana da kaso ko tsagi guda goma sha takwas:

- "Allahu Akbar" Sau (4)
- "Ashhadu an la'ilaha illallah" Sau (2)
- "Ashhadu anna Muhmammadar rasulullah" Sau (2)
- "Hayya alas salah" Sau (2)
- "Hayya alal Falah" Sau (2)
- "Hayya ala khairil amal" Sau (2)
- "Allah akbar" Sau (2)
- "La ilaha illallah" Sau (2)

## Yadda Ake Yin Iqama

Iqama na da matakai guda goma sha bakwai:

- "Allahu Akbar" Sau (2)
- "Ashhadu an la'ilaha illallah" Sau (2)
- "Ashhadu anna Muhmammadar rasulullah" Sau (2)
- "Hayya alas salah" Sau (2)
- "Hayya alal Falah" Sau (2)
- "Hayya ala khairil amal" Sau (2)
- "Qad qamatis salah" Sau (2)
- "Allah akbar" Sau (2)
- "La ilaha illallah" Sau (1)

Mas'ala ta 58:- Mustahabbi ne a yi salati ga annabi (s.a.w) yayin da aka faxi sunansa muxuakaki a cikin kiran salla da makamancinsa, ga wanda yake zance ko yake sauraro.

Mas'ala ta 59:- Yana da kyau a rava shaidawa da wilayar Imam Ali (a.s), ba tare da nufin cewa

shaidawar wani vangare ne na kiran sallar ko iqamar ba, kamar yadda wani sashin ruwayoyi suke tabbatar da hakan, misalin wannan shi ne abin da a lokacin Annabi, (s.a.w), a yayin da suka kashe, Hai'alatu wanda aka fi sani da Aswadul Ansi, wanda ya yi da'awar annabta bisa qarya, mai kiran sallarsu ya kasance yana cewa: Ash'haadu anna Muhammadan rasulullah, wa anna Hai'alat kazzabun. Ba tare da nufin cewa wani vangare ne na kiran salla ba.



Mas'ala ta 60:- A yayin kiran salla da iqama an sharaxanta wasu sharuxa kamar haka:

1. Kiran sallar ya gabaci iqama, banda akasin haka.

2. Ya zama an yi da yaren Larabci ingantacce, ba ya halatta a fassara ta da wani yaren daban.

3. Kiran sallar da iqamar su kasance bayan lokaci ya shiga, har ma ga wanda ya yi sallar raka'atul fajri shi kaxai a bisa ihtiyaxi na wajibi.

4. An sharaxanta a yayin iqama, mai iqamar ya kasance a tsaye kuma yana mai fuskantar alqibla, sannan ya zama ya tsarkaka daga hadasi.

Mas'ala ta 61:- Makaruhi ne ga mai kiran salla da iqama ya yi zance, musamman bayan ya ce 'qad qamatussalati'.

**Wajiban Salla**

1. Yin niyya
2. Yin kabbarar harama
3. Tsayuwa
4. Samun nutsuwa
5. Yin karatu
6. Yin zikiri
7. Ruku'u
8. Sujjada
9. Yin tasbihi
10. Sallama
11. Jerantawa
12. Yi daki-daki

**Na farko: Niyya:**

Abin da ake nufui da ita shi ne, mutum ya yi salla da niyyar neman kusanci zuwa ga Allah maxaukakai, irin yadda ya gabata a alwala.

Mas'ala ta 62:- Duk wanda ya yi salla da nufin mutane su yabe shi ko domin jin tsoron 'yan gidansu, to sallarsa ta vaci. Saboda haka matasa da samari na jinsin nan guda biyu, (wato maza da mata), ina jan hankalinsu da su faxaka a kan haka domin sallarsu ta zama da niyyar neman kusanci zuwa ga Allah maxaukaki, ba wai don saboda wani abu daban ba.

Mas'ala ta 63:- Ya wajaba ga mutum ya san yanayin sallar da yake sallata, misali sallar alfijir (Asuba), ko kuma sallar Azahar ko La'asar ko sallar Magariba da Issha'i.

Na biyu: Kabbarar harama:

Da ita ake fara salla, kuma salla tana vaci idan babu ita, a bisa mantuwa ko da gangan, kamar yadda tana vaci idan aka daxa ta da gangan. Idan aka karanta ta daidai, to bai halatta ga mai salla ya maimaita ta har sau biyu ba, saboda salla ta na vaci da daxa ta, don haka ta zama tilas ya zo da ta uku saboda ta zama ita ce ta farkon salla, (wacce salla zata inganta da ita).

Mas'ala ta 64:- Ya wajaba a yi kabbarar harama da yaren Larabci, ba ya inganta a yi fassararta da wani yaren na daban, kamar yadda ya wajaba a yi

ta ingantacciya, wani sashi na mutane suna karanta ta da wannan sigar (Allah wakbar), wannan kuskure ne da ya daxu, tilas ne a faxaka da shi a kuma nisance shi.

Mas'ala ta 65:- Mai salla yana da zavi na furta ta (kabbarar harama) a bayyane ko a voye a cikin dukkanin salloli.

Mas'ala ta 66:- A bisa ihtiyaxi na wajibi mai salla ya saurara kaxan kafin da kuma bayan ya yi kabbarar harama, kada ya sada ta da abin da ya gabace ta ko kuma ya biyo Bayan ta da wani abu kamar karatu.

Mas'ala ta 67:- Mustahabbi ne mai salla ya xaga hannayensa yayin kabbarar harama zuwa daura da kunnensa ko fuskarsa, idan ya cika kabbararsa sai ya saki hannunsa.

Na Uku: Tsayuwa:

Ya waba ga mai salla ya zama a tsaye yayin da zai yi kabbarar harama, da lokacin da yake karatu da kuma kafin ya yi ruku'u da bayansa, kafin ya tafi qasa zuwa sujjada. Ihriyaxi na wajibi ya tsaya akan qafafuwansa biyu ba wai a kan xaya kawai ba.

Mas'ala ta 68:- Wanda ya gajiya yin salla a tsaye saboda rashin lafiya ko makamancinta na daga uzurori, ya yi salla a zaune.

Na Huxu: Nutsuwa: Bisa ihtiyaxi wajibi: Wato mai salla ya zama a tsaye qyam ba motsawa a yayin kabbarar harama, da karatu da zikirin salla. Salla ba ta halatta ba a cikin mota lokacin da take tafiya a bisa ihriyaxi na wajibi, haka nan a cikin jirgi idan ya kasance yana yin girgiza a sakamakon kaxawar iska, saboda jiki yana kyarma sai ya rasa nutsuwa.

**Na Biyar Da Na Shida: Yin karatu da zikiri:**



A raka'ar farko da ta biyu sai ka karanta Fatiha da wata sura daban daga cikin sororin Kur'ani. A raka'a ta uku a sallar Magariba ko raka'o'in nan biyu na qarshe na sallar Azahar da La'asar da kuma sallar Isha'I mai salla yana da zavi tsakanin surar Fatiha ita kaxai ko kuma ya karanta tasbihat, ana karanta su da zikiri, ya isar cikin sallar a ce: "Subhanallahi, walhamdu lillahi wala ilaha illallahu wallahu akbar" kuma a

yi sau xaya ya wadatar, amma an fifita a maimaita sau uku.

Mas'ala ta 69:- Wajibi ne yin karatu a salla ya zama ingantacce, abin da aka qaddara shi ne, mai salla ya riqa komawa Kur'ani ya karanta surar da ya zava cikin tsari daidai da qa'idojin Larabci ingantattu.

Mas'ala ta 70:- Surorin nan guda biyu: Alam tara kaifa da Li'ilafi suna da hukuncin sura xaya, idan ka zavi ka karanta suratu Alam tara kaifa bayan ka karanta Fatiha, tilas ne ka karanta suratu Li'ilafi a bayanta. Haka ma surorin nan biyu wato suratu Duha da Alam nashraha, idan ka zavi ka karanta suratu Duha, babu makawa ka karanta Alam nashraha bayanta.

Mas'ala ta 71:- Kalmomin da qarshensu wasali ne ba xauri ba, idan kana son ka zarce ha haxe su da kalmomin da suke biye da su, to ana qaunar ka yi misali mimun xin nan na "arrahim" wacce ake mata harka da kisira, to idan ka zarce da kalmar "maliki" a misali, sai ka karanta kamar haka "Arrahmanir rahimi maliki".

Amma da a ce za ka yi waqafi a kalmar "arrahim", sai ka karanta ta haka "Arrahmanir

rahim" kana mai yi wa mimun xin xauri, haka za ka riqa aiwatarwa a kowace kalma.

Mas'ala ta 72:- Idan ba ka san yadda ake karatu ingantacce ba, to ka tabbata ka nemi sanin hakan kafin ka yi salla.

Mas'ala ta 73:- Ya wajaba ga mazaje su bayyana karatu a sallar Asuba da kuma raka'o'in farko da na biyu na sallar Magariba da Issha'i. Amman mata suna da zavi yayin karatun nasu da su bayyyana ko kuma su yi da sauti qasa-qasa.



Mas'ala ta 74:- Ya wajaba ga maza su voye karatu a sallar Azahar da La'asar da raka'a ta uku a sallar Magariba, da kuma raka'o'I na uku da na huxu na sallar Isha'i. Amma duka wannan banda "Bismillar rahmanir rahim", ita wannan mustahabbi ne ga maza su bayya karanta ta a raka'o'in farko da na biyu na sallar Azahar da La'asar.

Mas'ala ta 75:- Tabbas ya mai girma, za ka iya tambayar cewa, ya ya yanayin bayyanar da karatu

ko voyewa yake?, Don amsa tambayarka? Sai mu ce:

Shin ka tava dacewa da yiwa xan uwanka raxa a kunnensa, ta yadda ba wani mutum da yake jin ka?

To misalin irin wannan ya isar a cikin voyewa, ba wai kawai motsa levuka ba ne, dangane da bayyanawa kuwa yana isarwa mutum ya yi karatu kamar yadda yake yin zance a majalisi tare da abokansa ba tare da kururuwa ba.

Mas'ala ta 76:- Ya halatta mai salla ya buxa Kur'ani, ya karanta sura daga surorin Kur'ani don ka da ya auka cikin kuskure.

NA BAKWAI: Ruku'u:

Ruku'u ya halatta a cikinsa a riqa cewa: Subhana rabbiyal azim wa bihamdihi. Ko kuma ka faxi: Subhanallahi sau uku. Amma ihtiyaxi na wajibi ka zama tabbatacce ka da jikin ka ya riqa motsi yayin da kake tasbihi, kamar yadda ya gabata a kabbara da karatu.

Na Takwas: Sujjada:

A kan tafukan hannaye da gwiwoyi da manyan

'yan yatsun qafa, da kuma xora goshinsa a kan qasa ko wani abu na tsiro, ban da wanda ake ci ko ake sutura da shi, kamar yadda da zai zo nan gaba. Sannan ya halatta a sujjada mai salla ya riqa faxin: Subhana rabbiyal A'ala wa bihamdihi. Misali ya kuma halatta ya faxi: Subhanallahi sau uku, a maimakon na farko. Amma ihtiyaxi na wajibi ya zama tabbatacce a yayin da yake furta tasbihi.

Mas'ala ta 77:- A kowace raka'a sujjada biyu ce, sai ya yi sujjada bayan ya xago daga ruku'u, sannan ya zauna bayan ya yi sujjadar farko, sai kuma ya yi sujjadar farko kuma ya yi sujjadar karo na biyu.

Mas'ala ta 78:- Bai halatta qasar ta zama ta yi gangare sosai ba, sama da tsawon faxin 'yan yatsun hannun huxu ba, ta yadda tudun da ke tsakanin goshi da manyan 'yan yatsun qafa biyu, zai zama sama da tsawon faxin `yan yatsun haxu.

Mas'ala ta 79:- Ya halatta a xora goshi yayin sujjada a kan qasa, misalin tsakuwa da turvaya da tavo da siminti da wani abu na tsiro, da sharaxin kada ya zama wanda ake ci misalin tuffa ko wanda aka sanyawa kamar auduga, kuma ya wajaba bigiren yin sujjada ya kasance mai tsarki,

don haka ba zai xora goshinsa a kan najasa ba. Kuma akwai falala mai yawa da ta zo game da sujada kan turvayar kabarin Imam Husain (a.s), amincin Allah ya tabbata a gareshi, da abin da yake gefensa na qasar garin Karbala.

Na Tara: Tashah'hud:

Tahiya ma wajibi ce a raka'a ta biyu da ta huxu da kuma raka'a ta uku a sallar Magariba, wannan kuwa bayan sujjada ta biyu, kuma ya isar, a ce: "Ashhadu an la'ilaha illallahu wahdahu la sharika lahu, wa ashhadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluhu, Allahumma salli ala Muhammad wa aali Muhammad".

Na Goma: Sallama:

Ita ce ta qarshe a salla, ya isar wa mai salla ya ce: Assalamu alaikum. Abin da ya fi ya qara da: Wa rahmatullahi wa barakatuhu. Amma an fifita a haxe su, kuma mustahabbi ne kafin su, ka ce: Assalamu alaika ayyuhannan nabiyyu wa rahmatullahi wa barakatuhu.

Mas'ala ta 80:- Yin tasbihi a ruku'u da sujjada da tashahhud da kuma sallama ya halatta a cikin, ga maza da mata da su bayyana karanta su ko su

voye a dukkanin salloli.

Na Goma Sha Xaya: Jerantawa:

Misali mai salla ya fara da kabbarar harama, sai karatu, sai ruku'u, snanan ya xago kansa daga ruku'u, sai ya yi sujjada, haka nan zai yi. Bai halatta a gabatar da abin da yake a qarshe ya zama a farko ba, kamar a gabatar da sujjada, sannan ruku'u.

Na Goma Sha Biyu: Bibiya:



A bisa ihtiyaxi na wajibi, kada a rarraba tsakanin yanke-yanken salla da gangan ta yadda hakan zai kai ga warwarewar shakalin salla, duk wanda ya shagaltu da cin abinci -kamar dai yadda aka saba- a cikin sallarsa, to sallar sa ta vaci, a bisa ihtiyaxi na wajibi, amma haxiye `yan gutsattsarin tattakin abincin da ya yi saura a cikin baki ba ya cutarwa.

FAXAKARWA:



Mustahabbi ne a yi alquniti a raka'a ta biyu bayan an kammala karatu a kowace salla, kana mai xaga hannayen ka, kana mai yiwa kanka addu'a da kuma danginka da musulmai baki xaya.

Mas'ala ta 81:- Mustahabbi ne bayan an kamala salla ka yi sujjada kana mai cewa: Shukran Lillahi, sau uku a taqaice. Sannan mustahabbi ne ka yi tasbihin sayyida Zahara, amincin Allah ya tabbata a gareta; Shi ne: Allahu Akbar sau talatin da huxu (34), Alhamdu lillahi sau talatin da uku (33), Subhanallahi (33).



## Masu Vata Salla

Abubuwan da suke vata salla wasu al'amura ne wanda idan suka faru yayin da ake salla, sallar ta vaci, manya-manya daga ciki guda takwas ne:

Na farko: Idan abin da yake vata alwala ya faru ga masallaci, kamar rihi (tusa) ko fitsari ko gayaxi ko kuma bacci a yayin da yake salla, to sallar ta vaci.

Na biyu: kauce wa alqibla da gangan, idan mai salla ya qudurce cewa ga inda fuskancin alqibla yake, bayan ya yi sai ya gano kuskurensa a wajen ayyana alqiblar da ya yi, to idan bambancin ya zama bai wuce abin da ke tsakanin jihar dama ko hagun ba, zai yi hukunci da ingancin sallarsa. Idan kuwa ya zama sama da haka to ya sake ta.

Na uku: Yin zance da gangan, bai halatta masallaci ya riqa yin zance da irin zancen da aka saba yin a al'ada ba, amma karanta Kur'ani da zikirin Allah maxaukaki da yabon manzon Allah aminci ya tabbata a gareshi ba ya cutarwa.

Na huxu: Dariya, wacce ke xauke da sauti, (qyaqyatawa), amma yin murmushi kawai ba ya

cutarwa, haka nan yin dariya bisa mantuwa ko kuma bisa rashin sani, hukuncinta ba ya cutrwa.

Na biyar: A bisa ihtiyaxi na wajibi a bar yin kuka saboda wani al'amari na duniya, amma babu laifi da yin ta da gangan, idan domin wani al'amarin ne na lahira, Misalin jin tsoron Allah ko don qanqantar da kai, ko kuma don nuna shauqi a gareshi yayin sallar, amma idan bisa mantawa ne, wannan ba ya cutarwa.

Na shida: Bisa ihtiyaxi na wajibi a bar ci da sha da irin gwargwadon da aka sani a al'ada, amma haxiye yawu da abin da ya yi saura a baki na abinci ba ya cutarwa.

Na bakwai: Sanya hannu a qirji da nufin duqar da kai ga Allah maxaukaki bidi'a ne, an fare shi ne bayan Annabi tsira da aminci su qara tabbata gareshi, duk wanda ya zo da shi yana sane da hakan da nufin shar'ancinsa ko domin yaxa varna to sallarsa ta vaci, wanda kuwa ya aikata shi bisa rafkanuwa ko saboda taqiyya to sallarsa ba ta vaci ba.

Na takwas: Ganaganta faxin (amin) haramun ne. Ihtihaxi na wajibi sallar ta vaci, idan an yi shi da gangan.

Mas'ala ta 82:- Haramun ne a bisa ihtiyaxi na wajibi a yanke salla ba tare da wani dalili ba, amma ya halatta, idan mai salla ya buqatu zuwa yanke sallar bisa larura, ko ya yi shakka a cikin ingancinta, sai yake son ya yanke ta, domin ya sake ta, to ya halatta.

Mas'ala ta 83:- Idan mutum ya manta sallarsa sai ya tuna bayan lokacinta ya fita, to wajibi ne a kansa ya rama ta.

Mas'ala ta 84:- Idan mai salla a yayin da yake salla ya yi kokwanto, a kan cewa shin ya aikata vangaren (juzi'in) sallan da ya gabata ko kuwa bai yi ba, to ba zai yi la'akari da kokwantonsa ba, misali: Idan yana ruku'u sai ya yi kokwanton cewa shin ya karanta sura a bayan fatiha kuwa?, to ba zai yi la'akari da shi ba. Haka nan idan ya zama yana cikin tashahhudi bisa misali, sai ya yi kokwanto cewa shin sujjada xaya ya yi kuwa ko biyu? To ba zai yi la'akari da shi ba, ya ci gaba da tashahhudin sa.

Mas'ala ta 85:- Idan mutum ba shi da masaniyar cewa ya yi salla ne ko bai yi ba, to idan ya zama da sauran lokaci to ya wajaba ya yi sallar, idan kuwa lokacin ya qare to ba komai a kansa. Da zai

yi kokwanto kafin rana ta faxi, cewa: shin ya yi sallar Azahar ko la'asar, ko kuwa? ya wajaba a gareshi ya yi sallar, amma da rana ta faxi, sai ya yi kokwanto shin ya sallaci Azahar ko la'asar kuwa, ko kuwa?, to ba wajibi ba ne ya sallace su, saboda lokacin ya riga ya qare.

Mas'ala ta 86:- Idan mai salla ya yi kokwanto wajen aiwatar da wani vangare daga vangarorin salla, kafin ya tsallake muhallinsa ya shiga vangare na gaba da yake bin sa, ya wajaba a gareshi ya aikata wannan vangaren da yake kokwanto a kansa. Misali: Da ya kasance a tsaye sai ya yi kokwanton cewa shin ya karanta suratul Fatiha ko bai karanta ba? To ya wajaba a kansa ya karanta ta. Ko kuma idan ya kasance a zaune a raka'a ta biyu kafin ya yi tashahhud, sai ya yi kokwanton cewa ya zo da sujjada xaya ne ko biyu, ya wajaba a kansa ya zo da wata sujjadar daban kafin ya yi tashahhud xin.

Ka kula ya mai girma mimini da mumina masu daraja da wananan bambanci da yake tsakanin wannan mas'alar da abin da ya gabata a mas'ala ta (71) shi ne a waccan mas'alar. Kokwanton mai salla ya zama bayan ya shiga cikin vangare na gaba ne, a yayin da a wannan mas'alar kokwanton

ya zama kafin qare muhallin abin da yake kokwanto a kansa ne, ya kai ga shiga vangaren da yake bi masa, tilas ne a nan ya zo da vangaren kokwanton saboda bai tsallake muhallinsa ba.

## Sallar Jam'i

Ya zo a ruwaya cewa, lada mai yawa ya tabbata ga mai yin salla a jam'i, mustahabbi ne ga Musulmi ya riqa yin salla a jam'i ko da a gida ne, kamar yadda da sannu zai zo. Sai dai bai inganta mutum ya riqa yin salla a bayan kowane mutum ba, kai ya wajaba sashin sharaxai na jam'i su cika ga liman, mafi girma daga ciki biyu ne:

1. Limamin ya zama adali, ma'ana ya kasance mai addini, ta yadda yana hanuwa daga manyan-manyan savo, ta yadda da zai aikata savon a wani yanayi na ba zato ba tsammani, sakamakon rinjayar sha'awa, ko fishi, sai ya gauggautawa zuwa tuba. Amma idan savonsa ya yawaita to bai zama adali ba, kuma bai halatta a yi salla a bayansa ba.

2. Ya zama yana inganta karatu, wannan sharaxin ya kevanci sallar da ake bayyanawa ne kawai: Asuba, magariba, Isha'i. Idan mai bin ya zama ya shiga cikin sallar jam'i a raka'o'i biyun farko, -a bisa ihtiyaxi na wajibi-, amma a wasun waxannan sallolin kamar sallar da ake voye karatu to salla ta hallata a bayan wanda yake karatun bisa

kuskuren, sai mai bi xin ya yi karatu ingantacce da kansa a voye.

Mas'ala ta 87:- Bai halatta namiji ya yi salla a bayan mace ba, lalle ne ya yi salla a bayan namiji kawai, sai dai mace tana da damar ta yi sallar jam'i tare da namiji. Ya kuma halatta ta yi salla a bayan mace, ya cancanta ga yarinya misali ta yi sallar jam'i da mahaifiyarta, ta tsaya a daman mahaifiyarta.

**Sharaxan Jam'i**

Wasu al'amura ne waxanda idan suka tabbata dukkansu a sallar jam'i sai ya inganta, idan kuwa xaya daga cikinsu bai cika ba. Jam'I bai inganta ba. Muhimmai daga cikin su guda huxu ne:

Na Xaya: Kada ya zama tsakanin mai sallar da limamin jam'i ko tsakanin liman da sauran masu sallar akwai kariya, kamar Katanga.

Na biyu: Kada qasar da liman yake salla a kan ta, ta zama tana sama sosai da qasar da mamun da suke bayansa, suke kan ta, amma da a ce fifikon qasar bai kai 'yan yatsu uku ba, ko kuma da

fifikon mai hauhawa ne, wanda ba za a iya lura da shi ba, to ba ya cutarwa.

Na Uku: Kada mai salla ya nisanta da liman, ko sauran masu sallar waxanda ta hanyarsu ne zai qulla jam'in, amma da a ce tazarar ba ta kai mita xaya da xaya bisa huxu na mita ba, to ba ya cutarwa.

Na Huxu: Kada wajen tsayuwar mai salla (mamu) ya zama a gaban wajen tsayuwar liman, lalle a bisa ihtiyaxi na wajibi ya xan ja baya kaxan ko da gwargwadon 'yan yatsu huxu ne.

Na'am, idan mace ce limamiyar, mai binta sai ta tsaya daura da ita a cikin sahu xaya. Amma idan mace ta kasance tana bin salla a bayan namiji, to sai tsaya a bayansa.

## Hukunce-hukuncen Sallar Jam'i

Mas'ala ta 88:- Yin karatu a raka'o'i biyun farko ya saraya a kan mamu, ba zai karanta Fatiha da surar ba, amma ba ta saraya a kansa a raka'o'i na uku da na huxu ba, maimakon haka sai ya karanta fatiha ko kuma tasbihi a voye.

Mas'ala ta 89:- Bai halatta mamu ya zo da aikace-aikacen salla ba da gangan kafin liman, bai halatta ya yi ruku'u ko ya xago da kansa kafinsa ba, ko kuma ya yi sujjada kafin ya yi ba, sai dai ya halatta ya yi tasbihi ko tashahhud kafinsa.

A misali kada ya xago da kansa daga sujada kafin liman ya xago da kansa, sai dai ya halatta ya furta tashahhud kafin liman ya furta.

Mas'ala ta 90:- Mai girma mai karatu namiji da mace masu daraja, sallar jam'i tana da lada mai yawa, kada ku haramta wa kanku wannan ladan. Kana da damar ka yi sallar jam'i a bayan wasu sashi na ahalinka, waxanda suke da riqo da addini, don haka xa yana iya yin sallar jam'i, a bayan mahaifinsa ko xanuwansa, ko kuma 'ya a bayan babanta ko babarta. `Ya`ya mata kuwa sai su zama bayan bayan 'ya'ya maza a sallar jam'i.

Amma abin da ya fi a yi salla a bayan malami adali, domin ya zo a cikin hadisi daga Imam Sadiq (a.s) ya ce: Yin salla a bayan malami daidai take da yin salla raka'a dubu a bayan waninsa.

## Sallar Juma'a

Ita wajibi ce a zamanin da imami (a.s) yake a sarari, amma a zamanin da yake voye kamar yadda yake a zamaninmu wannan, to mai salla yana zavi na ya yi ta ko ya yi sallar Azahar, tun da ita ce ba ta inganta a yi ta a xaixaiku ba, ballantana ma tana inganta ne a jam'i, don haka zamu xora nauyin yi bayaninta akan manyan littattafan fiqihu, mu taqaita a kan bayanin hukunce-hukuncen da suke da alaqa da mamu, ta hanyar abubuwa masu zuwa:

1. Tilas ne a sami tattaruwan sharaxan limamin jam'i a limamin Juma'a, bai halatta a yi ta a bayan fasiqi ba.

2. Ya haramta ga wanda ya halarci sallar Juma'a ya yi zance a yayin da liman yake huxuba, kai yana da kyau mamu ya miqa saurarensa zuwa gareta.

3. Duk wanda bai riski huxubobi biyu ba, ya isar masa idan ya riski sallar tare da liman, kai ko da kuwa wani sashi ya riska na sallar -a bisa bayanai filla-filla da aka faxa a cikin littattafan fiqihu-.

4. Ba a qulla sallar Juma'a guda biyu, alhali tazarar da ke tsakaninsu ba ta kai kilo mita (6) ba. Idan aka riga yin xaya daga cikin su, kuma ta zamo, ta cika sharaxanta to ta biyun ta vaci.

A nan, ya zama dole mu yi nuni bisa cewa: Haqiqa sallar Juma'a wani sababi ne kuma hanya ce ta wayar da kan muminai, da shiyar da su, da ilimantar da su addininsu, da ba su tarbiyya, da kuma faxakar da su a kan maslaharsu, da maslahar musulunci da qasashen Musulumai, ba wai sallar ta zama wani dalilin rarrabuwarsu da watsewarsu ba, da kuma soke-soken juna a tsakaninsu, a cikin tsarkakan abubuwan da suka haxa da su ba.

**Sallar Matafiyi**

Idan mutum Musulmi ya yi tafiya, ta yadda nisan tafiya zuwa da dawowa ya kai kilomita arba'in da shida (46), to sai sallolin da suke masu raka'a huxu su koma raka'a biyu, kuma ana kiran ta (sallar QASARU). Misali mutum ne ya yi tafiya zuwa wani gari wanda nisansa da garinsa ya kai kilo mita ashirn da biyar wajen tafiya, to ya zama wajibi, ya yi qasarun salla mai raka'a huxu, saboda idan an tattara tafiyar tasa zuwa da dawowa ta yi daidai da kilo mita hamsin.

Akwai wasu adadi na sharaxai na sallar qasaru, a yayin tafiya, da za mu faxe su, daga cikin su akwai:

i. Kada mai tafiya ya yi niyyar zai yi kwana goma a garin da ya tafi.

ii. Kada tafiyarsa ta zama ta savo, kamar taimakon azzalumai ko kasuwancin giya da sauran abubuwan savo. Akwai wasu bayanai filla-filla amma nan ba mahallinsu ba ne.

**Sallar Ramuwa**

Sallar da mutum bai sallace ta a lokacinta ba, ana kiranta da sallar ramuwa, misali mutum ne bai farka daga barcci ba domin sallar Asuba, ya wajaba ya rama ta daga baya. Haka nan idan ya manta bai sallaci wata salla ba a lokacinta ya wajaba ya rama ta daga baya.

Mas'ala ta 91:- Idan ya zama mutum ba ya yin salla har tsawon wani zamani, daga baya sai yake son ya tuba, to sai ya nemi gafarar Allah ya kuma rama sallolin da bai yi su ba, kafin ya tuba, idan kuma bai san adadin yawanta ba, sai ya isu da gwargwado mafi qaranci. Misali idan bai san cewa ana neman gwargwadon wata xaya ne ko biyu ba a wajensam to sai ya isu da rama sallar gwargwadon wata xaya.

**Sallar Ayoyi**

Ita salla ce da ta wajaba yayin da rana ko wata suka yi kusufi (suka kisfe), haka nan ko aka yi iska mai tsananin duhu da makamancinta, idan har hakan ya bayar da tsoro a bisa xabi'ar mutane. Haka nan yayin girgizar qasa a bisa ihtiyaxi na wajibi.

Sallar aya raka'a biyu ce, a kowace raka'a ana yin ruku'u biyar. Ya wadatar ya zo da ita a bisa tsari mai zuwa:

Zai fara yin sallar da yin kabbarar harama (Allah Akbar), ya karanta Fatiha, sannan ya zavi wata sura daga Kur'ani. Misali suratul Qadri, sai ya karanta aya xaya a cikinta bayan ya karanta Fatiha; Misali:

Bismillahir Rahmanin Rahim, Inna an zalnahu fi lailatin qadr. Sai ya yi ruku'u. a ruku'un ya ce: Subhana rabbiyal azim wa bihamdihi. Sai ya xago kansa ya karanta aya ta biyu kawai ta wannan surar, ba tare da ya karanta fatiha ba. Misali "Wama adra ka ma lailatul qadr". Sai ya yi ruku'u irin wanda ya yi da farko. Ya sake karanta aya ta gaba, ya sake yin ruku'u irin na farko, har sai ya

kai ayar qarshe a wannan surar wato aya ta biyar, wato 'Salamun hiya hatta maxla'in fajr', Sai Ya Yi Ruku'u Irin Wanda Ya Yi Da Farko, Sannan ya xago kansa ya yi sujjada guda biyu kamar yadda ake yi a sallolin yau da kullum.

Sai ya miqe ya yi raka'a ta biyu, ya karnata Fatiha, bayanta ya karanta xaya daga cikin surori, yana mai rarraba ta, ya yi irin yadda ya yi a raka'a ta farko. Bayan ya kammala raku'u gudan biyar, sai ya xago kansa ya yi sujjada biyu, ya yi tashahhud, ya yi salla kamar yadda aka saba a sauran salloli. Da haka ne sallar aya ta qare.

Mustahabbi ne a yi alqunuti kafin a yi ruku'u na biyu da na huxu da na shida da na takwas da kuma na goma. Ya kuma halatta a taqaita yin alqunutin a sashen wasu raka'o'in.

Mas'ala ta 92:- Wajibi ne a aiwatar da sallar ayoyi a yayin da ake kusufi xin, kada mutum ya jinkirta har sai kusufin ya qare.

FAXAKARWA

Idan kusufin rana da wata ya zama cikakke,

amma mutum bai san hakan ba, wajibi ne a kansa ya rama sallolin ayar, haka nan idan bai yi sallar ba da gangan a tsawon rayuwarsa sai ya tuba, ya wajaba a kansa ya rama abin da ya kuvuce masa na sallar aya. Akwai bayanai filla-filla da aka yi a litattafai na fiqihu.

## Nafilolin Yau Da Gobe

Salla ta mustahabbi ana kiranta da nafila, akwai lada daga Allah ga wanda ya sallace ta, nafiloli suna da yawa, daga cikinsu akwai na yau da kullum, su ne:

• Raka'a biyu ta nafila kafin sallar asuba.

• Raka’a takwas, nafilar Azahar kafin sallar Azahar.

• Raka'a takwas nafilar La'asar, kafin sallar Laza'asar.

• Raka'a huxu, nafilar Magariba bayan an sallaci Magaribar, salloli biyu ne, kowace xaya raka'a biyu.

• Raka'a biyu a zaune bayan sallar Isha'i, ana kiranta da nafilar Isha'i.

Waxannan su ne nafilolin yau da kullum, yin su yana da lada mai yawa, an fifita Musulmi ya lazimce su, ko da kuwa da abin da ya sauwaqa ne.

TAMBAYOYI

1. Mene ne sharaxan da suka wajaba a same su a tufafin mai salla?

2. Idar har mai salla bai san cewa igiyar agogonsa na fata ne ta xabi'a ba, ko kuma ta qirqira ce ba, shin salla ta halatta da ita?

3. Waxanne halaye suka halatta a yi salla tare da najasa?

4. Waxanne al'amura ne suka wajaba a salla?

5. Ka qirga abubuwan da suke vata salla.

6. A yayin sujjada sai ka yi kokwanton cewa ka yi raka'a ne ko kuwa, shin za ka yi la'akari da kokwanton a farko.

7. A lokacin da kake tsaye a raka'a ta biyu ba ka san cewa ka karanta Fatiha ko ba ka karanta ba, to yaya za ka yi?

8. Ya idan tana son ta yi sallar jam'I tare da uwarta, shin za ta tsaya a daman uwartata ko a bayanta?

9. Ka qirga adadin sharaxan jam'i.

10. Meye nisan tafiyar da ake qasarun salla mai raka'a huxu?

11. Shin ya halatta mamu ya xago kansa kafin liman.

12. Shin kana sallar nafila? Mece ce ita? Idan ba ka sallatarta meye dalili? Ka yi qoqarin kawar da shi, domin ka sami ladan nafila.

**Azumi**

Azumi yana daga mafi girman wajibi a kan mutum, lokacin yin sa a watan Ramadan ne, daga hudowar alfijir zuwa faxuwar rana. Amma ana qaunar a jinkirta zuwa faxuwar jaja-jajan nan na gabas.

Sai mutum ya nisanci dukkan ababen ci, wanda da sannu za mu faxe su a nan gaba kaxan.

Mas'ala ta 93:- A qarshen wata Sha'aban, idan mutum ya ga jinjirin wata ya wajaba a gareshi ya yi azumi. Haka nan idan maza biyu adalai suka gan shi, amma idan mutum bai gan shi ba da kansa, kuma adalai biyu maza ba su gan shi ba, sannan shi kuma bai san akwai jinjirin watan ko babu ba, to ba wajibi ne ya yi azumi ba a rana ta biyu wacce ake kira da ranar kokwanto (yaumush shakk), idan kana son ka azumce ta, to kada ka yi niyyar azumin watan Ramadan.

Mas'ala ta 94:- Bai halatta a qarshen rana a watan Ramadan mutum ya ci abinci ba, har sai bayan ya tabbatar da rana ta faxi ko kuma ya dogara a kan sallar wanda yake amintacce ko shaidar adalai biyu, amma zaton ranar ta faxi ba

ya isarwa.

Mas'ala ta 95:- Ya wajaba mutum ya yi azumi da niyyar neman kusanci zuwa ga Allah, yin azumi ba ya inganta a sakamakon jin tsoron dangi ko saboda mutane su yabe shi, ko kuma ya riqa alfahari a gaban su, irin wannan azumin ya vaci, Allah ba ya karvarsa, kuma zai yi maka hisabi a kansa a ranar alqiyama.

Ya zo a cikin hadisi daga manzon Allah amincin Allah su tabbata a gareshi, dangane watan Ramadan ya ce: Ku roqi Ubangijinku da niyya ta gaskiya da kuma zuciya mai qaranta littafinsa, domin shaqiyyi shi ne wanda aka haramta masa gafarar Allah a wannan wata mai girma. Kuna yunwarku da qishirwarku ta cikin Ramadan, ta riqa tuna muku da ranar alqiyama da qishirwarta, Ku ba da sadaka ga talakawanku da miskinanku... har zuwa qarshe.

**Masu Karya Azumi**

Su ne abubuwan da suke sa azumi ya vaci, kuma guda goma ne:

Na xaya da na biyu: Ci da sha komai qanqantarsu.

Na uku: Yi wa Allah da Annabi (s.a.w) qarya, ko xaya daga cikin imamai amincin Allah ya tabbata a gareshi, duk wanda ya yi qarya da gangan ya cirato wani abu daga manzon Allah tare da ya yi imani da cewa ba haka ba ne (qarya ne), azuminsa ya vaci, kuma ya zama mai savo da wannan qaryar da ya yi. Haka nan a bisa ihtiyaxi na wajibi azumin ya vaci, idan mutum ya ba da labari ba tare da ya tabbatar da ingancin labarin ba.

Na huxu: Shan taba, a bisa ihtiyaxi na wajibi.

Na biyar: Ganganta yin amai, da rana, a watan Ramadan, na sa azumi ya vaci, amma idan ya ganganta yin hakan a sakamakon rashin lafiya, to ya halatta a gareshi, sai ya rama azuminsa daga baya. Na'am, idan amai ya yi masa ba zata, ba bisa zavi ba, to ba ya vata azumi.

Mas'ala ta 96:- Idan wani abu ko sauran abinci ya fito daga ciki ya xago zuwa cikin baki, ya halatta a haxiye shi, kuma azuminsa bai vaci ba.

Na shida: Yin xura ko qarin ruwa (ta baki ko ta hanci ko ta dubura) da ruwa ko wani abu mai ruwa-ruwa, amma wanda yake busasshe idan har ba ya zagwanyewa cikin jiki ba, to ba abin da zai hana wannan, amma wanda yake zagwanyewa a cikin jiki kamar maganin da yake na tattare da mai to abisa ihtiyaxi na wajibi ya nisance shi. Amma idan mara lafiya ya buqatu zuwa gareshi ya yi amfani da shi, ya kuma kame bakinsa a wannan ranar, sai ya rama azuminsa.

Na bakwai: Mutum ya jawo mani da kansa.

Na takwas: Da gangan mace ta wanzu a kan haila ko janaba har zuwa huxowar alfijir a watan Ramadan. (wato ta qi yin wankan su, har zuwa wannan lokacin)

Mas'ala ta 97:- Ya halatta a xora xige-xigen ruwa a kan ido ko kunne, amma maganin nan da ake xigawa a hanci, idan har ba ya zarce wa zuwa ciki (daidai inda abinci yake narkewa) ta hanyar maqogoro, to ba ya cutar da azumi, amma idan ba haka ba azumi yana vaci.

Mas'ala ta 98:- Ya halatta a haxiye yawun baki ko da ya zama mai yawa, haka nan majina, duk da an fi son a tofar da shi.

Mas'ala ta 99:- Yin allura a tsokar jiki ko jijiya, ba ya vata azumi, haka nan yin allurar da ke xauke da sinadirin abinci, ya halatta ba kuma ya vata azumi.

Mas'ala ta 100:- Amfani da kirfa a kowane irin yanayi, daidai ne ta hanyar hanci ne ko ta hanyar baki ya halatta, ba ya vata azumi ko da ya kai zuwa cikin huhu, matuqar ba ya kai wa zuwa ga manarkar da ke rarraba abinci ba.

Mas'ala ta 101:- Bai halatta a yi amfani da cingam xin da yake samun sa a ko'ina a cikin kasuwanni ba, saboda a cikinsa akwai kemikal na sukari ko kuma shi kan sa sukarin a cikinsa, kuma yana dagargajewa ta hanyar tattaunawa, sannan ya zarce cikin ciki.

Mas'ala ta 102:- Idan mutu ya manta cewa yana azumi sai ya amfana da sashin abinci to azuminsa bai vaci ba. A misali duk wanda ya sha ruwa, sannan daga baya ya tuna cewa shi mai azumi ne, to azuminsa bai vaci ba.

Mas'ala ta 103:- Bai halatta mutum ya qudurce

cewa ya karya azuminsa, da rana a watan Ramadan ba, ko da kuwa bai yi abin da zai karya masa azumi ba.

Mas'ala ta 104:- Ya halatta ga mai azumi ya sanya turare a jikinsa da tufafinsa, ya kuma shaqe shi, azuminsa ba ya vaci da haka.

**Halayen Cin Abinci**

Su wasu yanayoyi ne da ya halatta ko ya wajaba a ci abinci a cikin su, manya-manya daga cikinsu guda biyar ne.

Na xaya: Mara lafiya idan azumi na qara masa rashin lafiyar, to Allah bai xora masa yin azumi ba. Allah maxaukaki ya faxa a cikin littafinsa mai girma: "**Allah yana sonku da sauqi, kuma ba ya nufinku da wahala**" Baqara:185.

Amma idan azumi ba zai cutar da rashin lafiyarsa ba, to bai halatta ya ci abinci ba.

Na biyu: Mace mai haila.

Na uku: Matafiyin da sharaxai huxu suka tabbata a kansa:

1. Tafiyar tasa ta zama ta kai kilo mita (46) ko sama da haka.

2. Ya yi niyyar tafiyar kafin alfijir.

3. Ya yi tafiyar kafin zawali.

4. Kada tafiyar tasa ta zama ta savo. Kamar taikamon azzalumai ko kasuwanci na haram. -

Akwai bayanai daban-daban a cikin manyan littattafan fiqihu-.

Mas'ala ta 105:- Idan mai azumi ya yi tafiya bayan Azahar zai ci gaba da azumin na sa, kuma ya inganta, don haka bai halatta ya ci abinci ba.

Na huxu: Yawan shekara daga tsofaffi maza da tsofaffi mata, idan azumi zai musu wahala sosai.

Na biyar: Mai ciki idan azumi zai wahalar da ita ko zai cutar da jaririnta, haka nan mai shayarwa mai qarancin nono, idan har azumi zai cutar da nononta, ta yadda zai qaranta sosai, ko kuma ma ya yanke ba kuma zai dawo ba daga baya.

**Ramuwa Da Fidiya Da Kaffarori**

Haqiqa za a iya tambayar ka a ce: Mene hukuncin wanda ya ci abinci da rana a watan Ramadan, kuma mai zai aikata? Amsa ita ce, akwai bayanai dalla-dalla:

1. Idan mutum ya zama yana da uzurin cin abinci, musali, mara lafiya wanda azumin yake cutar da shi, ya wajaba ya rama azumin kwanakin da ya ci dalilin rashin lafiyarsa, idan ya zama ya ci abincin kwana biyar ne, to sai ya azumci kwana biyar bayan idin sallar fixir (salla qarama).

2. Mara lafiya da makamancinsa wanda ba zai yiwu su rama azumi ba, tsowon shekara har wani Ramadan na sabuwar shekara ya zo, to bai wajaba a gareshi ya rama ba. Sai dai maimakon kowacce rana da ya ci, zai ba da giram (870) na abinci ga talakawa, wannan abin da zai bayan shi ake kira; fidiya.

3. Wanda ya ci abinci da gangan bisa savo, ba tare da uzuri ba, ya wajaba ya rama bayan waxancan kwanakin da ya ci abincin a cikinsu, kuma ya wajaba a kansa ya ba da kaffara a madadin kowace rana da ya ci da gangan, abin da

muke nufi da kaffara a nan ya azumci wata biyu a jere, ko ya bayar da abin da ya kai (870) na giram xin abinci ga faqirai sittin, (ko wane faqiri 870 Gram) a madadin kowace ranar da ya ci abincin, idan ya ci abincin rana biyu ne da gangan, to ya wajaba ya rama su bayan idi, sai ya azumci wata huxu ko ba da abincin ga faqirai xari da ashirin, ko ya azumci wata biyu a madadin kowace rana ya ba da abinci ga faqiri sittin a madadin rana ta biyu…, akwai bayanai dalla-dalla da aka ambata a cikin littattafan fiqihu masu zurfi.

Mas'ala ta 106:- Yin azumin a ranar idin fiddakai da kuma ranr idin layya, haramun ne.

**Zakkar Fidda-kai**

Abin da ake nufi da ita, shi ne, ba da abinci ko kuxi wanda mai gida yake bayarwa a ranar idin fidda-kai ga kansa da kuma duk wani mutum da yake qarqashinsa, har da jariri qarami, ga muminai talakawa. Misalin abin da yake wajibi shi ne a bayar da kilo uku da rabi na abinci ko kuma abin da ya yi daidai da qimarsa ta kuxi, a madadin kowane mutum xaya na xaixaikun iyali. Idan gaba xaya adadin iyali tare da mai gidan mutum biyar ne, to sai ya ba da kilo goma sha bakwai da xigo biyar na abinci, kuma zai bayar xin ne ranar idin kafin sallar azahar kuma kafin ya sallaci sallar idi. Misali zai iya bada, alkama ko dabino ko shinkafa ko kuma hatsi (dangin qwayoyi daban). Idan kuma kuxi zai bayar sai ya zavi kalar abincin da zai bada qimar kuxin na sa ga mumini talaka. Na daga dabino ko alkama ko shinkafa ko makamantansu.

Mas'ala ta 107:- Duk wanda ba xan bani hashim ba ne, zakkar fixda kai da ya fitar ba ta halatta ga talakan Banu Hashim, abin da ake nufi da Banu hashim shi ne, duk zuriyar Hashim wato kakan manzon Allah, wato 'ya'yan Ali da 'ya'yan Aqil da

'ya'yan Abbas, xan Aliyu xan Abi Xalib amincin Allah ya tabbata a gareshi, da wasunsu na daga jikokin Hashim.

**Zakka**

Zakka xaya ce daga cikin wajibai na Musulunci wadda Kur'ani mai girma da sunna suka yi qarfafa a kanta. Zakka ta kasu kashi biyu:

1. Zakkar kuxi: Ita wajiba ce, a cikin abubuwa guda tara: dukiyoyi guda biyu: wato Zinare da Azurfa. Da dangin dabbobbi guda uku, su ne: raqumi da Qanana dabbobi (wato Tumakai da awakai) da kuma dangin shanu, wanda ya haxa da bakoloji.

Da shuka guda huxu, su ne: Alkama, da sha'ir, da dabino, da zabibi.

A koma cikin littattafan fiqihu masu zurfi donin sanin bayanin hukunce-hukuncensu.

2. Zakkar fidda-kai.

**Khumusi**

Shi wani haqqi ne da Allah maxaukaki ya farlanta shi, kuma nassin Kur'ani da sunna su ka yi magana a kansa.

Ya zo a hadisi daga Imam Musa Alkazim (a.s) ya ce: Na rantse da Allah, haqiqa Allah ya sauqaqa wa muminai arziqoqinsu da dirhami biyar, su sanya wa ubangijisu xaya, su kuma su ci guda huxun ababan halattawa. Sannan ya ce: Wannan yana daga cikin maganganunmu masu wahala kuma masu wahalarwa, ba wanda zai iya yin aiki da shi, ya kuma iya jorewa a kansu, sai wanda aka jarabci zuciyarsa da imani. Wasa'ilus Shi'a: j 9/ 485.

Khumusi yana wajaba a wurare guda bakwai, amma a nan za mu yi nuni da wurare biyu daga ciki:

Na xaya: Dukiyar da ta cuxanya da haram, bisa sharaxin kada ya zama za a iya bambance na haram daga na halal xin ba, kuma ba a san mai shi ba. To idan mai dukiya ya bayar da khumusin kuxin da muka faxa, sauran ya halatta ga mai shi.

Na biyu: Abin da ya ragu na kayan amfanin mutum a cikin shekara, na daga abin da ya zo masa na riba, amma banda gado, sai ya bayar da khumusin wannan dukiyar a yayin da shekarar khumusinsa ta zo.

Mas'ala ta 108:- Ana kasa Khumusi gida biyu: Kashi na farko ana kiransa da rabon imami (a.s), xayan kason kuma ana kiransa da kason sharifai. Duka biyun dole ne a cikinsu a koma zuwa ga mujtahidi adali, masani, kuma amintacce ga wuraren da za a yi amfani da shi a bisa haqqi na shari'a da aka ambata a wurarensa.

Mas'ala ta 109:- Dole ne ga mujtahidi adali ya yi amfani da khumusi a wurare na shari'a, dangane da kason Imam Mahadi (A.J.) ya tabbata ya yi amfani da shi a wuraren da ya tabbatar akwai yardar Imam Mahadi Almuntazar (a.s), ya sarrafa khumusi a cikinsu. Misali:

a) Yaxa koyarwar addinin Musulunci, da qarfafa xaliban ilimin addini da masu tabligi, waxanda suke riqo da addini, da amfanar da waxanda suka shagaltu da karantarwa da masu koyo, ko kuma isar da saqon addini, da yi wa muminai hidima.

b) Magance larurorin muminai talakawa masu

addini, idan haqqi na shari'a ya taskace wajen magance larurorinsu. Shi kuwa kason sharifai, sai ya riqa ba da shi ga muminai talakawa na 'ya'yan Hashim.

Dukkannin waxannan mujtahidi masani, adali, amintacce wajen sarrafa shi ga haqqi na shari'a da muka ambata, shi ne zai iyakance shi kamar yadda muka gabatar. Bai halarta ga mutum ya riqa gaugawar sarrafa khumusinsa ba, ba tare da koma wa zuwa ga mujtahidi ba. Akwai bayanai dalla-dalla masu yawa da aka ambata a cikin littattafan fiqihu.

TAMBAYOYI

1. Shin ya halatta a ci abinci idan mutum ba shi da tabbas da cewa rana ta faxi ko kuwa?

2. Idan majina ta zarce cikin baki, shin ya halatta a haxiye ta?

3. Idan ka manta da cewar kai mai azumi ne, sai ka sha ruwa, shin azuminka ya vaci?

4. Su waye waxanda ya halatta ko ya wajaba su ci abinci?

5. Mene ne sharaxan cin abinci ga matafiyi?

6. Mene ne gwargwadon Fidiya?

7. Mece ce Kaffara? Kuma a kan wa ta wajaba?

8. Shin ka tava bayar da khumusi a rayuwarka? Saboda me?

9. Ga wa ake ba da khumusi?

## Umarnin Kyakkyawa Da Hanin Mummuna

Umarni da kyakkyawa da kuma hani ga mummuna suna daga cikin wajibai, waxanda musulumci ya qarfafa a kansu. Allah maxaukaki ya ce:

“Kuma lalle ne ya zama a cikinku akwai wasu jama’u da za su riqa kira zuwa ga aikata alheri, da umarni da kyakkyawa da hani ga abin qi, irin waxannan su ne masu rabauta”. (Aali Imrana: 104).

Ya zo a cikin hadisi maxaukaki cewa: Kada ku bar yin umarni da kyakkyawa da kuma hani ga mummuna, sai ashararranku su shugabance ku, a sannan, idan ku ka yi addu'a ba za a amsa muku ba.

Kamar yadda ya wajaba a kan mutum ya lazimci wajabi, kuma ya bar abubuwan da suka haramta. Haka nan ya wajaba a gare shi, ya umarci wanda yake sakaci da wajibai, da ya yi riqo da shi, ya kuma yi hani ga wanda yake aikata haram da ya bar aikatawa.

Za mu faxi wasu adadi na wajibai da siffofi

kyawawa, -a matsayin shimfixa- kamar yadda za mu faxi wasu adadi na abubuwan da suka haramta, da kuma ayyuka munana marasa kyau, waxanda ba su dace da mutum ba. Daga misalai na kashi na farko, waxanda su ne abubuwa masu kyau:

1. Dogaro ga Allah maxaukaki, da kuma neman taimako daga gareshi, duk wanda yake dogaro da Allah to ya isar masa.

2. Salla da azumi da Khumusi da makamantansu suna daga rassan addini, ya wajaba a kan kowane mutum ya riqa yin riqo da su, ya kuma umarci wanda yake sakaci da su da riqa yin riqo da su.

3. Haquri: yana da nau'o'i daban-daban:

i. Haquri a kan Bala'i: Abin ya zama lalle ya kuma kamata shi ne; Mutum ya riqa yin haquri, idan aka jarabce shi, misalin rashin lafiya ko kurkuku ko talauci da makamantansu, kada ya riqa maganganun da ba su dace ba, saboda ya sami ladan masu haquri, domin Allah maxaukaki yana cewa: **"Kaxai za a cika wa masu haquri ladansu ba tare da hisabi ba"**. (Zumar: 10).

Ya zo a cikin hadisi daga manzon Allah (s.a.w):

Haquri kashi uku ne: Hauqiri yayin masifa, da haquri yayin biyayya, da kuma haquri yayin savo.

Ba wai ma'anar haquri shi ne wai kada mutum ya yi qoqarin kawar da cutuwa da bala'i a kan sa ba, maimakon haka, abin da yake akwai shi ne, a bisa misali; marasa lafiya, su riqa komawa zuwa ga likita har ya warke, sai dai idan warkewar ba ta tabbata ba, ko ta yi jinkiri to ya yi haquri kada ya yi ta yin raki. Haka nan talaka abin da aka wajabta masa shi ne; ya yi qoqari ya nemi aiki, har sai ya kuvuta daga talauci, sai dai idan bai yiwu ba saboda wani dalili, to kada ya yi ta raki ko kuma ya riqa magana, ko wani aiki da bai dace da Musulmi ba, maimakon haka ya yi haquri saboda ya sami ladan masu haquri.

ii. Haquri a kan bin Allah (s.w.t), misalin mai azumi yana fama da qishirwa a watan Ramadan, amma duk da haka yake yin haquri har sai ya kammala azuminsa, haka ma mai yin jihadi a tafarkin Allah, zai yi ta yin haquri da musibar yaqi.

iii. Haquri a kan barin yin savo, misali mutum ne yake tsananin son abin wani domin biyan buqatar kansa, amma duk da haka sai ya haqura, ya qi

sace kayan, saboda sata haramun ce.

Ya zo a cikin hadisi daga Imam Abu Abdullahi Sadiq (a.s), ya ce: Idan ranar qiyama ta zo, wasu mutane (wata jama'a ta mutane) za su zo qofar gidan aljanna, su buga qofa, sai a ce da su, su waye ku? Sai su ce: Mu ne ma'abota haquri. Sai a ce da su: A kan me kuka yi haqurin? Sai su ce: Mun kasance masu haquri a kan biyayyar Allah, mun yi haquri a kan barin sava masa. Sai Allah mai girma da xaukaka ya ce: Sun yi gaskiya, ku shigar da su Aljanna. Shi ne fassarar faxin Allah maxaukaki: "K**axai za a cika wa masu haquri ladansu ba tare da hisabi ba**".

4. Kyawawan halaye, wato halaye na gari, wato abin da ya wajaba ga Musulmi shi ne: halayensu su zama masu kyau tare da 'yan uwansu da sauran mutane, ya riqa girmama manya, ya riqa jin tausayin qananan raya, kada ya riqa wulaqanta mutum, kada ya cutar da mutane, kuma kada ya riqa murtuke fuskarsa ga mutane, kada ya riqa xaga sautinsa, ta yadda zai cutar da maqotansa domin ya sami yardar Allah maxaukaki.

Ya zo a cikin hadisi daga manzon Allah, amincin Allah ya tabbata a gareshi, yana cewa:

“Na hore ku da kyawawan halaye, domin kyawawan halaye su na kai mutum aljanna babu makawa, ina yi muku kashedi da miyagun halaye, domin miyagun halaye su na kai mutum wuta babu makawa).

A cikin wani hadisin daban, manzon Allah (s.a.w) ya ce: (Mafi kusancinku a gare ni a wajen zama a ranar alqiyama, mafi kyautatawar ku ga ahalinsa).

Ya kai mai karatu da makaranciya masu girma, shin ba kwa so ku kasance kusa da manzon Allah a cikin al'janna?

5. Taimakon mumini mai rauni da duk mutum wanda yake buqatar taimako, Allah zai tausaya maka, zai yarda da kai.

Ya zo a cikin hadisi cewa, manzon Allah (s.a.w), ya yi wa Imam Ali (a.s) wasiyya yana mai cewa: "Ya kai Ali, wanda ya isar wa maraya, ya ciyar da shi da dukiyarsa har ya wadata, to aljanna ta wajaba a gareshi". Ya kai mai girma, ka tsururuci aljanna ta hanyar taimakon maraya da dukiyarka har sai ya yalwata.

Ya zo a wani hadisi daga Imam Baqir (a.s), ya

ce: "Abu huxu duk wanda ya kasance a cikinsu Allah zai gina masa gida a aljanna: Duk wanda ya ba wa maraya mafaka, ya ji qan raunana, ya tausasa wa iyayensa, ya yi musu 'imfaqi' da dukiyarsa, ya kuma tausaya wa bayinsa".

Ya zo a hadisi daga manzon Allah (s.a.w) ya ce: “Muminai 'yan uwan juna ne, sashinsu yana biyan buqatar sashi..., za a biya buqatarsu ranar alqiyama".

6. Girmama Iyaye: Domin abin da ya zama farilla ga mutum Musulmi shi ne: ya riqa girmama iyayensa, ya saurari zancensu na daga abin da ya dace da biyayya, da kuma kyakkyawar mu'amala, kada ya keta wani haddi a gare su. Allah maxaukaki yana cewa: “**Kada ka ce da su kaico, kuma kada ka kyare su, ka faxa musu zance mai daxi**”. (Isra'i: 23).

Ya zo a hadisi: Aljanna tana qarqashin qafar uwaye. Idan ka girmama mahaifiyarka da mahaifinka, suka yarda da kai za ka cancanci aljanna, da yardar Allah maxaukaki.

7. Tsafta: Musulunci ya qarfafa, yin tsafta ta dukkanin nau’o’inta da kalolinta, ya kuma yi hani a kan dukkanin nau’o’in datti da qazanta. Ya zo a

cikin hadisai daga Annabi (s.a.w) ya ce: (Ku yi tsafta iya iyawarku, domin Allah ya gina Musulunci a kan tsafta, kuma -har abada- babu wanda zai shiga aljanna sai mai tsafta.

A wani hadisi, daga manzon Allah (s.a.w) ya ce: (Tir da bawa mai qazanta).

A cikin wani hadisi daga Imam Ali (a.s) yana cewa: (Wanda ya tsarkake tufafinsa, baqin ciki da vacin rai ko damuwa na gushewa daga gareshi, kuma tsarkakke ne a cikin sallarsa).

A sashin wasu nassoshi an xamfara talauci da datti: Ya zo a cikin hadisi daga Imam Ali (a.s) ya ce: Ku tsarkake gidajenku daga yanar gizo-gizo, domin barinta yana gadar da talauci.

Akwai wasu nassosi daban-daban masu yawa, da suke kwaxaitarwa a kan tsafta da sanya turare da kuma nisantar datti da qazanta, sai dai abin takaici, yadda muke ganin sakaci mai yawa daga musulmai dangane da tsaftace jikinsu da yaxuwar datti da qazance-qazance a cikin gidajensu, da titunansu da ma cikin biranensu, wanda wannan ya haifar da yaxuwar talauci da cututtuka iri-iri. Haka nan wannan lamarin ya bayar da mummunar sara kuma ya bayyanar da mummunar fuska,

game da Musulunci da musulmai.

Abin da ake fata, kowa ya himmantu da tsafta ta dukkanin nau'o'in ta, da kuma zuburar da wasu a kanta, domon xabbaqa koyarwar Musulunci.

Akwai ayyuka na gari da siffofi masu yawa da aka ambace su a litattafai masu zurfi.

Daga cikin misalai a kashi na biyu, wanda shi ne abin qi:

1. Zalunci, shi ne keta iyakar wasu, to shi yana daga mafi girman abubuwa da suka haramta. Ya zo a cikin hadisi daga Imam Baqir (a.s) ya ce: "Yin zalunci a duniya duhu ne a lahira...".

A wani hadisin kuma daga Imam Husaini (a.s) cewa, yayin da ya yi wa xansa Imam Zainul Abidin (a.s) wasiyya a ranar Ashura, yana mai cewa: (Ya kai xa na, na hane ka da zaluntar wanda ba shi da mai taimako a kanka, sai Allah).

Qari a kan haka, cewa addu'ar wanda aka zalunta a kan wanda ya zalunce shi, Allah maxaukaki yana amsa ta.

Ya zo a hadisi daga manzon Allah (s.a.w) cewa: (Addu'ar musulmin da aka zalunta karvavviya ce).

Yana daga cikin ire-iren zalunci abin da yake gudana a tsakanin sashin iyalai, na ta'addancin uba a kan 'ya'yansa, ko kuma ta'addancin 'ya'ya a kan iyayensu, da kuma ta'addacin miji a kan matarsa, ta yarda cin moriyarta a sakamakon rauninta, ko kuma akasin haka. Haka nan ta'addancin babban xa ko kuma babbar 'ya a kan qananan yaran gida. Duk waxannan suna daga cikin zalunci da aka haramta, wanda kuma Musulunci bai yarda da shi ba,-yana qin sa-. Haka nan yana daga cikin zaluncin uba ya tilasta wa 'yarsa auren wanda ba ta son sa.

2. Taimakon azzalumai komai qanqantar wannan taimakon to haramun ne. ya zo a hadisi: Mafi sauqin abin da Allah zai yi wa wanda ya taimaki azzalumi ranar alqiyama shi ne: (Ya sanya shi a cikin wani kewaye, misalinsa kamar babbar hema na daga wuta, har sai ya gama yi wa sauran halittu hisabi). Allah maxaukaki yana cewa: **Ku yi taimakekeniya a kan biyayya da taqawa, kada ku yi taimakekeyi a kan zunubi da ta'addanci**. (Ma'ida:2).

3. Qarya haramun ce a shari'a, kai takan koma zuwa ciwon zuciya da mutum ya kan samu. Domin maqaryaci yakan iya sabawa da qarya, sai

wata rana ya kunyata a gaban mutane, su wulaqanta shi, daga nan ba za su tava kuma gasgata shi ba, har sai ya dawo ya zama mai gaskiya. Hakan kuma bai dace da Musulmi ba.

Ya zo a hadisi daga Imam Al-Baqir (a.s) cewa: Qarya tana ruguza imani. To ta yaya mutum Musulmi zai yarda ya ruguza imaninsa?.

4. Cin naman wani (wato giba), shi ne a tona asirin mumini a bayan idonsa, saboda a zubar da qimarsa da kuma bayyanar da aibinsa. Misali idan ka san cewa abokinka ya aikata wani kuskure to kada ka kai wannan abin ga wasu, don soke mutuncinsa da qimarsa. Maimakon haka, ka yi masa nasiha da kada ya qara yin wannan kuskuren, idan kuwa har ya qara yi wato ya dage a kansa, to ka sanar da mahaifinsa ko kuma wani mutum mai girma a wajensa, saboda ya hana shi ba tare da ka kunyata shi a tsakanin mutane ba.

Mas'ala 110:- Faxar aibun wani, ya halatta a halaye masu zuwa, da za mu ambata:

a) Wanda yake bayyanar da fasiqanci, idan yana haka alfarmarsa ta faxi, faxar aibunsa kuma ya halatta.

b) Wanda aka zalunta, to shi ya halatta ya bayyana zaluncin da aka yi masa ga mutane, ko da bayyanarwar zai lazimta tona asirin wanda ya zalunce shi xin.

c) Masu shigo da bidi'a cikin addini, su waxannan ya halatta a tona asirinsu da bayyanar da bidi'ar ta su, domin mutane su guje su, kada su tasirantu da su.

5. Mu'amala da miyagun abokai, su ne irin abokan nan da ba sa riqo da addini da tarbiyya.

Abin da ake fata shi ne mutum ya yi musu nasiha ya umarce su da aikata abu mai kyau, ya kuma hane su da abin qi, idan hakan bai amfanar ba to ya bar yin mu'amala da su, domin kada ya tasirantu da yanayinsu.

Ya zo a hadisi: Ya kasance idan shugaban muminai Imam Ali (a.s) ya hau mimbari ya kan ce: Ya kamata Musulmi ya nisanci yin abota da mutum uku: Mai ruwayar fajirci wanda ya shagaltu da wasa kuma yake aikata munanan ayyuka, da wawa; wato dolon da ba ya ganewa, da maqaryaci.

6- Zage-zage da furta zantuka marasa kyau masu

muni, domin bai dace da mutum Musulmi ba.

Ya zo a hadisi daga manzon Allah (s.a.w) cewa: (Lallai Ubangiji ya haramta aljanna a kan dukkanin mai yaxa alfasha, mai miyagun kalmomi, mai qarancin kunya). Ma'ana wanda ya saba da furta kalmomi munana, haqiqa aljanna ba mazauninsa ba ce. ya zama lalle mutum ya nisance su idan har nasiha ba ta amfane su ba, don kar mutum ya koya daga garesu ya yi asarar aljanna.

7- Fushi, da yawa zaka ga mutum na yi abubuwan da ba su dace ba, da hujja cewa yana cikin fushi ne, amma wannan hanzarin ba karvavve ba ne, a shari'ance. Ya zo a cikin hadisi daga Imam Sadiq cewa: "Fushi shi ne mabuxin dukkanin sharri", domin mai fushi baya yin tasarrufi da hankalin sa, a shirye yake da ya aikata sharri da kuskure a qarqashin tasirin fushi.

8- Kwaxayi: shi ne mutum yaqi yarda da abin da Allah ya bashi, ya riqa kwaxayin abin da ke hannun mutane, haqiqa irin wannan bai dace da mutum musulmi ba, ballantana ma wannan yana sa mutum ya rasa alherin duniya da na lahira, don haka za ka ga makwaxaici ya rasa alherin duniya

saboda bai gamsu da abin da Allah ya bashi ba, domin kullun qari yake hanqoro, kuma ta yiwu ma ya yi hasarar lahira, domin kwaxayinsa zai iya jansa zuwa varna ko ha'inci ko wani aiki na laifi.

9- Yin wasa da jiki domin fitar da maniyyi: Shi ne mutum ya yi wa kansa abin da zai sa maniyyi ya fita daga jikinsa ta hanyar wasa, da al'aurarsa ko makamancin haka, ba bambanci, mace ce ko namiji.

10- Tabarruji (rashi rufe jiki da bayyana al'aura ga mata), haqiqa idan mace ba ta lazimci kyakkyawar shiga da kuma hijabi (wato rufe jiki) ba, ta cancanci azaba mai raxaxi a ranar alqiyama.

Ya zo a wani hadisi daga manzon Allah amincin Allah ya qara tabbata a gareshi, cewa "A mi'irajinsa zuwa sama ya ga wasu mataan rataye su da gashin su, suna cikin azaba mai tsanani, a yayin da Faxima (a.s) ta tamabaye shi sababin yi musu azaba, sai ya ce: Amma wacce aka rataye ta da gashin kanta, ta kasance ba ta rufe shashin ta daga maza".

A wani hadisin kuma, daga gareshi mai tsira da amincin Allah, cewa "Ya hana mace yin ado ga wanda ba mijinta ba, idan ko ta aikata, Allah ya yi

alqawarin zai qona ta da wuta”.

11- Kasala da raki, haqiqa mai yin su zai yi asarar duniya da lahira, domin zai yi ta sakaci da abin da ya wajaba a gareshi da kuma abin da zai amfane shi.

A wani hadisi daga Imam Kazim (a.s), yana mai yin wasici ga shashin `ya`yansa da shi: “Kuma na hane ka da kasala da raki, domin suna hana ka samun rabonka na duniya da na lahira”.

Abinda ya wajaba shi ne mutum ya sabawa kansa da ayyuka, da himma da juriya har sai ya cimma gaci a rayuwarsa, kuma ya samu daraja maxaukakiya a lahira.

12- Riya shi ne mutum ya yi nufin nema da samun yabon mutane da ibadar da ya yi, ba neman kusanci da biyayya ga Allah ba, wannan yana daga cikin mafi girman haramun, kuma mai yin riya na rasa rabonsa na duniya da na lahira. An rawaito a wani hadisi daga manzon Allah animcin Allah ya tabbata gareshi, haqiqa mai yin riya za a kira shi a ranar alqiyama da sunaye huxu: ya kai kafiri, ya fajiri, ya mayaudari, ya hasararre, ayyukanka duka zasu xaixaice kuma ladanka ya rushe, ba ka da makuvuta a yau, ka nemi ladan ka

daga wanda kake yin aiki dominsa".

13- Yi wa mumini algush: shi ne nuna masa wani abu bisa savanin yadda yake, bisa misali; ya bayyana munanan kaya a matsayin kaya masu kyau.

Ya zo a cikin hadisi, daga Annabi amincin Allah ya qara tabbata a gareshi, ya ce "Ku saurara lalle duk wanda ya yi mana algush ba ya daga cikin mu" ya faxi hakan har su uku.

Waxannan wasu misalsali ne daga kyawawan ayyuka – wajiba daga cikin su da kuma mustahabbai -da kuma misalsali daga abin qi mummuna- na haram ne ko kuma makruhi. Kuma horo da wajibi da kuma hani daga haram, wajibi ne. kuma horo da mustahabbi da hani a bisa makruhi wannan kuwa abin so ne ba wajibi ba ne.

TAMBAYOYI

1- Qididdigo biyar daga cikin abubuwa kyawawa, kuma ka faxi wanda ka ke aikatawa?

2- Qididdigo goma daga cikin munana?

3- Shin kana aikata wani munkari, idan har kana aikatawa, shin ka xauki matakin barin sa?

4- Faxi hadisi xaya game da alfasha?

5- Faxi hadisi a kan mu'amala da abokai munana?

6- Ambaci hadisi a kan zalunci?

7- Mece ce illar fushi faxi hadisi a kan sa?

8- Ambaci hadisi a kan azabar wacce ba ta rufe jikinta?

9- Idan ya faru cewa abokinka ya yi qarya, ta yaya zaka yi masa nasiha da ya bari?

10- Faxi hadisi a kan azabar mataimaka azzalumai?

11- Shin kana kula da tsaftar jikinka da tufafinka da zuciyarka?

12- Shin xakin da kake zaune a cikinsa da gidan da unguwar da birnin dukkaninsu tsaftattune? Kuma shin ka taimaka wa wasu a wajen tsaftace su, idan har ba ka bayar da gudummawa ba, tu ta wajaba ka gaggauta zuwa yin hakan tare da sauran 'yan gidan ko kuma `yan unguwa.

13- Shin ka tava yi wa `yan gidanku ko kuma abokanka nasiha a kan tsafta?

## Hukunce-hukuncen Hijabi

Mas'ala ta 111: bai halatta ga yaro da yarinyar da suka balaga ba, su gaisa, sai idan sun kasance `yan’uwan juna, kuma `yan’uwan juna su ne:

Uba, da uwa, da kaka ta-vangaren uba da vangaren uwa, da kuma baffa, da gwaggo ta vanaren nasu.

Xa da `ya.

Miji da babansa da xansa.

Mata da babarta da yarta.

Baffofin uba da gwaggogin sa ta vabgaren uwa da uba.

Baffofin uwa da gwaggogin sa ta vabgaren uwa da uba.

Xan’uwa da `yar’uwa da kuma `ya`yayen su maza da mata.

Don haka bai halatta ga namiji ya gaisa (yin hannu) da matar da ba makusanciyarsa ba, kuma bai halatta ba ga mace ta gaisa da namijin da ba makusancinta ba.

Mas'ala ta 112: `Yar'uwar mata ba ta daga cikin makusanta, don haka bai halatta a yi hannu da ita ba, kuma ya wajaba ta sa wa mijin `yar'uwarta hajibi.

Mas'ala ta 113: ya wajaba ga mace da da kuma yarinyar da ta balaga ta sanya hijabi ga ta kuma rufe dukkanin jikinta a gaban wanda ba makusanci ba in banda fuska da tafuka biyu, kuma ihtiyaxi na wajibi ta rufe qafafuwanta.

Mas'ala ta 114: Ya halatta ga mace ta cire hijabin ta a gaban makusanci na jini da na surukuta, kuma ya wajaba ta suturta al'aurarta, Kamar yadda ihtiyaxi na wajibi kar ta wuce iyaka -ta bayyana jikinta, tare da bayyana abin da zai kawo fitina-.





**Bakance Da Rantsuwa**

Mas'la ta 115: idan mutun baligi ya rantse -namiji ne shi ko mace- da Allah cewa zai aikata wani abu ko ya yi bakance ga Allah (s.w.t), ya wajaba a gareshi ya cika shi, idan har bai lazimci wannan ba to ya yi savo, kuma kaffara ta wajaba a gare shi kuma dole ne ya tuba daga savon.

Mas'la ta 116: Bakance da rantsuwa kaxai suna qulluwa ne bisa sharaxai masu zuwa:

1- Ya yi furuci da lafazin bakance ko rantsuwa, yin niyyar su kaxai ba zai isar masa ba.

2- Su kasance ga Allah (s.w.t) sai mai rantsuwar ya ce bisa misali, na rantse da Allah zan aikata kaza, mai bakance kuma ya ce: na yi wa Allah alqawari zan aikata kaza.

Amma bakance da kuma yin rantsuwa da Annabi amincin Allah ya tabbata gareshi da alayen sa, ko kuma Kur'ani mai girma, ko ka'aba maxaukakiya ko imami amincin Allah ya tabbata a gareshi, waxannan duka ba bakance ko rantsuwa na shari'a ba ne, ta yadda kaffara zata hau kan mutum a sakamakonsu. Kaxai wannan xorawa kai

alqawarin aikatawa ne kuma mustahabbi ne mutum ya lazimci abin da ya alqawarta wa kansa da shi.

3- Rantsuwar yaro ba ta qulluwa sai da izinin mahaifinsa kamar yadda rantsuwar mata ba ta qulluwa har sai da izinin mijinta, savanin bakance, haqiqa shi bakance yana qulluwa kuma ya hau kansu, ba yare da yanda ko goyen bayan uba da miji ba, mutuqar bai ci karo da haqqinsu ba.

4- Ya zama abin da aka rataya rantsuwar da bankancen abin da shari'a ta yarda da shi ne, kamar wajibi da mustahabbi da kuma abu mai amfani. Ba sa qulluwa idan suka rataya da haramun ko makruhi ko wani aiki mai cutarwa, wanda ya yi ratsuwa a kan shan giya ko shan taba ko barin salla ko wani abu na wargi, to rantsuwarsa ba ta qullu ba.

5- Mai rantsuwar da mai bakancen su kasance sun xaura niyyar yin hakan, bisa zavinsu, kuma suna masu nufin yin hakan da maganarsu, wanda azzalumi ya tilasta shi a kan yin rantsuwa ko kuma ya yi yana cikin halin maye, to rantsuwarsa ba ta qullu ba haka ma bakance.

Mas'ala ta 117: Idan sharaxan ingancin bakance

da na rantsuwa suka cika sai kuma ma'abocinsu ya karya alqawarin, yana sane, da gangan, to ya savi Allah (s.w.t) kuma ya wajaba a kansa ya tuba kuma ya yi kaffara, ita ce ta qosar da miskinai goma, ko dai ta hanyar qosar da su, ko kuma ya ba su kimanin giram 780, na abinci bisa ihtiyaxi na wajibi, ya zamo daga dangin alkama ko garinta, ko gurasart. Ko kuma ya tufatar da su ta hanyar saya musu tufafin da za su ishe su, wanda kuma ba zai iya ciyarwar ko tufatarwar ba, sai ya yi azumi uku.

Mas'ala ta 118: idan ya yi rantsuwa yana mai qarya a kan faruwar wani abu, ya yi savo kuma ya wajaba a gareshi ya tuba, amma kaffara ba ta wajaba a gareshi ba.

Mas'ala ta 119: An karhanta yin rantsuwa ta gaskiya, kuma lalle a nisanci yin rantsuwa ta wasa, wacce ake ta yaxawa a shashin wasu al'ummu.

**Halattattun Abubuwan Ci**

Dabbobi sun kasu kaso uku:

Na farko: Dabbobin da suke rayuwa a ruwa, cin su bai halatta ba in banda kifi mai vawo ko kwasfar da za a iya kankarewa, shin ya kasance babba ne ko qarami, kamar rubiya ko karfasa, d.s.s. Amma idan ya kasance mara vawo da kwasfar da za a iya kakkarewa kamar juri, ko tarwaxa, ko hutu, to bai halatta a ci namansa ko a ci kitsensa ba,

Na biyu: Daga cikin dabbobin doron qasa na gida, ya halatta a ci naman raqumi da shanu da tumakai da awakai da barewa, haka ma jakin daji da vauna da ragon daji, kuma an karhanta cin naman doki da alfadari da jakin gida.

Mas'ala ta 120: Ya haramta daga cikin dabbobin doron qasa dukkanin dabbar da take da fiqa misalin zaki da dila, haka ma qananan qwari kamar kwarkwata da tururuwa da qudan zuma, haka ma ya haramta a ci macijiya da veran dinka da duk vera, da zomo, da damo, da makamancin haka na daga abin da aka ambata a cikin littattafan fiqihu.

Na uku: Tsuntsaye, idan ka kalli tsuntsu a sama a yayin da ya tashi, za ka ga shashinsu, na motsa fikafikansa, sama da qasa a mafi yawan lokuta, kamar irin su benu da tattabara, a yayin da za kaga wasu dangogin suna yin shawagi da fikafikan su a mafi yawan lokuta, kamar su shaho da shirwa. Don haka kaso na farko halal ne, kaso na biyu kuma haramun ne, kuma haramun ne cin jemage da xawusu da hankaka, da kuma dukkanin tsuntsayen da suke farauta, kamar shaho da mikiya. Sai dai ya halitta a ci tsuntsun da aka sani, (wato aka san halaccinsa) koda kuwa an san cewa yana farautar kifi.

Mas'ala ta 121: Haramun ne cin qwarin da suke tashi, kamar qudan masai da quda da makamantansu.

Mas'ala ta 122: An haranta cin `ya`yan marenan dabbobi da saifa, ihtiyaxi na wajibi nisantar laka, amma vargon da ke cikin qashi ya halatta a ci shi, kuma akwai wasu abubuwan da aka haramta, an ambace su a cikin littattafan fiqihu dalla-dalla.

Mas'ala ta 123: An haramta cin duk wani abu da ya najastu, haka ma tavo an haranta cin sa, im banda wani xan qanqanin gwargwadon da bai

wuce girman qwayar alkama ba, na daga qasar Imam Husain amincin Allah a gareshi, domin neman waraka, kuma ya halatta cin xan kaxan daga baqin da ke ciki tawada.

Mas'ala ta 124: Shan giya ya haramta da ma dukkan abin da ke sa maye, ko da kuwa ya kasance mai tsarki ne, kamar yadda shan tsumin inabi ma haramnu ne, sai sai idan aka tafasa shi a kan wuta har sai da biyu bisa ukun sa ya gushe ya zama xaya bisa uku ne ya yi saura, to a wannan yanayin ne kawai ne ya halatta a sha shi.

Mas'ala ta 125: Mustahabbi ne wanke hannaye kafin cin abinci, haka ma yin bisimilla, ita ce ka ce "Bismillahir rahmanir rahim" da ci da dama da kuma wanke hannu bayan ci, da kuma yin hamdala ga Allah (s.w.t). "Alhamdu lil-Lahi".

**Yanka**

Yanka, shi ne: abin da zai sanya naman dabba ya zam halal:

Mas'ala ta 126: Idan aka fitar da kifi daga cikin ruwa a raye, ya halatta a ci namnsa, kuma ya zama tsarkakke, kuma ba a sharxanta xan su -mai kamun kifi- ya zama musulmi ba, idan kafiri ya yi su, kuma ya fitar da shi a raye, ya halatta. Akwai qarin bayanai da aka ambata a cikin littattafan fiqihu.

Mas'ala ta 127: Tsutsaye da dabbobin doron qasa, idan ka cire raqumi, namansu ba ya halatta sai har in wasu sharaxai sun tabbata a wajen yanka shi, mafi mahimmancinsu guda biyar ne, kamar haka:

1- Mai yankan ya kasance musulmi.

2- Yankan ya kasance da wuqar qarfe.

3- Yanke jijiyoyi huxu, wato maqoshi (hanyar abinci) da maqogoro (wato hanyar shaqar numfashi) wanda yake a qarqashin maqoshi, da kuma jijiyoyin wuya guda biyu, waxanda suke a

geffan maqogoro da maqoshi,

4- Fuskantar da dabba zuwa alqibla.

5- Ambaton sunan Allah a yayin yankan kamar yace “Bismillah ko Allahu akbar” ko makamancin wannan. Godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikai.

TAMBAYOYI

1- Waxanne abubuwa ne aka haramta?

2- Waxanne tsuntsaye ne suka halatta a ci naman su?

3- Shin ya halatta a ci 'ya'yan marena da al'aurar dabbobi?

4- Idan kafiri ya farauci kifi shin ya halatta a ci?

5- Ambaci sharaxan yanka dabbar doron qasa?

6- Daga qarshe shin ka amfana daga mas'aloli da hukunce – hukuncen da muka bayyana maka?

Na gode maka kuma Allah ya yi maka albarka.

**Kammalawa**

Zuwa nan ne, waxannan jerin na littattafan taqaitattu su ka zo qarshe, waxanda na rubuta su ne a cikin wani yanayi na tsanani na musamman, da manufar wayar da matasa da sabon jini a kan hukunce-hukuncen musumulci, ina mai roqon sa maxaukaki da ya datar da mu baki xaya a wajen lazimtar hukunce-hukuncen addininmu madaidaici, da kuma yin hidima ga al'ummarmu da kuma qasarmu. Haqiqa shi mai ji ne,mai amsa roqo.

An rubuta shi a cikin kurkukun mai mattsanancin tsaro na musamman "Abu Guraib". A shekarar 1409 bayan hijira.

Hujjatul Islam Sayyid Riyadh Hakim

Sadaukarwa........................................................................5
Gabatarwa..........................................................................7
Tushen Addini....................................................................11
Rassan Addini....................................................................16
Alamomin Balaga Na Shari'a....................................................19
Ijtihadi (Qoqari) Da Taqalidi (Bibiyar Fatawa)..............................22
Najasosi...........................................................................27
Masu Tsarkakewa.................................................................35
Alwala..............................................................................47
Sharuxxan Alwala.................................................................53
Masu Vata Alwala.................................................................55
Taimama...........................................................................58
Janaba..............................................................................66
Wanka..............................................................................68
Jinin Haila.........................................................................71
Salla.................................................................................72
Lokutan Salla Da Adadinta......................................................76
Tufafin Mai Salla..................................................................78
Alqibla..............................................................................83
Yadda Ake Yin Salla..............................................................84
Wajiban Salla......................................................................89
Masu Vata Salla..................................................................100
Sallar Jam'i.......................................................................105
Sallar Juma'a.....................................................................109
Sallar Matafiyi....................................................................111
Sallar Ramuwa...................................................................112
Sallar Ayoyi.......................................................................113
Nafilolin Yau Da Gobe..........................................................116
Azumi..............................................................................119
Masu Karya Azumi..............................................................121
Halayen Cin Abinci..............................................................125
Ramuwa Da Fidiya Da Kaffarori..............................................127
Zakkar Fidda-kai.................................................................129
Zakka..............................................................................131

Khumusi ........................................................................ 132
Umarnin Kyakkyawa Da Hanin Mummuna.............................. 136
Hukunce-hukuncen Hijabi ....................................................... 153
Bakance Da Rantsuwa ............................................................ 155
Halattattun Abubuwan Ci ....................................................... 158
Yanka ..................................................................................... 161
Kammalawa ............................................................................ 164